رسائل للحجاج والمعتمرين
باللغة الهوساوية

# SAKO ZUWA GA ALHAZAI DA 'YAN UMRA

NA

**SHEIKH, DR. YAHYA BIN IBRAHIM AL-YAHYA**

**FASSARAR**
**ABDURRAHMAN SANI YAKUBU ZARIA**
**(JAMI'AR MUSULUNCI TA MADINA)**

## *FIHIRISA*


GABATARWA............................ 1

SAKO NA FARKO...................... 4

SAKO NA BIYU.................. 19

SAKO NA UKU......................... 37

SAKO NA HUDU...................... 59

SAKO NA BIYAR..................... 65

SAKO NA SHIDA..................... 78

SAKO NA BAKWAI................. 85

SAKO NA TAKWAS ................ 90

SAKO NA TARA ...................... 104

SAKO NA GOMA ..................... 110

بسم الله الرحمن الرحيم

## GABATARWA

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai, kuma na shaida babu abin bauta bisa cancanta sai Allah majibincin mutanen kwarai, kuma na shaida Annabi Muhammad (S.A.W) bawanSa ne kuma Manzonsa, shugaban masu fararen fuskoki ranar kiyama (saboda hasken alwala), na shaida lalle ya isar da sakon da Allah ya aiko shi, kuma ya bayar da amanar da a ka ba shi, kuma ya yi wa al'umma nasiha, kuma ya barmu a kan wata hanya fara kal, daren (wannan hanyar) kamar rana yake babu bambanci, babu wanda zai karkace daga wannan hanya face hallakakke, ya Allah ka yi dadin tsira da aminci gare shi, tare da mutanen gidansa da sahabbansa,da wanda ya yi kira irin kiransa, kuma ya bi sunnarsa kuma ya bibiyi sawunsa, kuma ya tsaya a kan hanyarsa har zuwa ranar sakamako.

Bayan haka:

Ya kai dan'uwana Alhaji, wanda Allah Ya zabe shi a tsakanin miliyoyin Musulmi, domin ziyarar dakinSa mai alfarma, ina rokon Allah da ya jibinci al'amuranka a duniya da lahira, kuma ya sanya ka mai albarka duk inda kake.

Ya kai dan'uwa mai girma, ya kai wanda ka gamu da wahalhalun tafiya, kuma kayi hakuri da su, kuma ka fitar da dukiyarka, kuma ka bar gidanka, ka yi bankwana da iyalinka da 'ya'yanka, ba don komai ba sai domin sauke faralin da Allah ya dora maka, na ziyarar dakinSa mai alfarma, Allah ya sanya hajjinka karbabbe ne, kuma ya gafarta maka zunubanka, ya rufa maka asiri.

Ya dan'uwana Alhaji, saboda son da nake maka da sha'awar da kake bani, tare da farin cikina da zuwanka, da jin dadina da kubutarka, ya sa na fuskance ka da wasu sakonni, saboda in sauke wani wajibi da ya hau kaina, game da kai, kuma in kasance na bi umurnin Allah da ya ce:

"وتواصوا بالحق وتواصوا بالصبر"(العصر ٣)

Ma'ana: Kuma suka yi wa juna wasiyya da gaskiya, kuma suka yi wasiyya da hakuri. (asr 3)

Kuma in bi umurnin masoyinmu, shugabanmu, abin koyinmu, Annabinmu Muhammad (S.A.W) da yake cewa: "Misalin Muminai wurin soyayyarsu da jin kan junansu, da suke yi, kamar misalin jiki daya ne, idan wata gaba ta kamu da cuta, sai sauran jikin ya kamu da zazzabi da rashin barci". Manzon Allah (s a w) ya sake cewa: "Mumini ga dan'uwansa mumini, kamar gini ne sashinsa ne ke karfafa sashi".

Dan'uwana Alhaji ina fata za ka saurari sakonnin dan'uwanka mai kaunarka, kuma mai tausayinka ina fatar Allah zai sa su yi maka amfani.

## SAKO NA FARKO

Dan'uwana Alhaji, kar ka manta da abin da ya kawo ka wannan gari, wato hajji, ka sani cewa shi hajji da ma sauran ayyuka baki daya, Allah ba ya karba, sai aikin ya zama domin shi a ka yi, da haka ne za ka samu ladan aikin, Allah yana cewa:

"وما أمروا إلا ليعبدوا الله مخلصين له الدين" (البينة ٥)

Ma'ana: "Kuma ba a umurce su da kome ba, face su bauta wa Allah, suna masu tsarkakeaddini gare shi, suna masu karkata zuwa addini gaskiya…" (bayyinah 5)

Kuma kafin a karbi aiki dole ne ya zama an yi aikin dai-dai, bisa sunnar Manzon Allah (S.A.W), Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: "Duk wanda ya aikata wani aiki (don kansa) ba tare da umurninmu ba, to an mayar mishi da aikinsa."

Ya kamata tunaninka kullum ya kasance: Shin an karbi aikinka ko ko a a?

Maganar aikin hajji kuwa Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: "Ku koyi aikin hajjinku a

wurina". Wato duk abin da nayi a cikin aikin hajji to kuma ku yi irin sa, kada ku kago wani abu daga wurin ku.

Aikin hajji mafi kyau da Musulmi zai yi, shi ne yayi shi yadda Manzon Allah (s a w) ya koyar, don ya yi katari da soyayya daga Allah tare da gafararSa. Allah yana cewa:

"قل إن كنتم تحبون الله فاتبعوني يحببكم الله ويغفر لكم ذنوبكم"(آل عمران٣١)

Ma'ana: "Ka ce: idan kun kasance kuna son Allah, to ku bi ni, Allah zai so ku, kuma ya gafarta muku zunubbanku". (Al Imran 31)

Saboda haka ya wajaba a kanka – ya kai dan'uwa Alhaji – ka koyi hukunce-hukuncen aikin hajji, kuma ka tambayi malamai kafin ka fara.

Yanzu zan ambata maka takaitacciyar siffar Hajji da Umrah. Amma ya kamata ka karanta abin da malamai suka rubuta (a kan Hajji da Umrah)

**SIFFAR UMRAH:**

1. Idan ka zo mikati, idan da hali, to, kayi wanka kamar yadda mai janaba yake wanka, sa'an nan ka sanya turare mai kamshi, idan kana da iko, (a jikinka ba a kayan Ihrami ba), daga nan sai ka sanya kayan Ihrami (gyauto da mayafi, farare), mace bata da kayan Ihrami (kayadadde), zata sa tufafin da ta ga dama, ba tare da ta bayyana kwalliyarta ba, kuma ba tare da ta yi kama da maza ba. Sai kayi haramar Umrah (haramar umrah ita ce kace:

"لبيك عمرة" LABBAIKA UMRAH). sa'an nan ka fara TALBIYYA kamar haka:

"لبيك اللهم لبيك، لبيك لا شريك لك لبيك إن الحمد والنعمة لك والملك لا شريك لك."

LABBAIKAL LAHUMMA LABBAIKA, LABBAIKA LA SHARIKA LAKA LABBAIKA, INNAL HAMDA WANNI'MATA, LAKA WAL MULK, LA SHARIKA LAKA.

Ma'ana: Na amsa kiranka ya Allah, na kuma amsa kiranka, na amsa kiranka ya Allah, ba ka da abokin tarayya, dukkan yabo da ni'ima da mulki naka ne, ba ka da abokin tarayyah.

Ihrami daga mikati wajibi ne, ba ya halatta ka wuce mikati (kana da nufin hajji ko umrah) face sai ka yi Ihrami.

2. Idan ka shiga cikin Ihrami, to ka sani akwai wasu abubuwa, da suka Haramta a gare ka kamar haka:

- Gusar da wani gashi a jikinka, saboda fadin Allah (s w t):

"ولا تحلقوا رؤوسكم حتى يبلغ الهدى محله"(البقرة ١٩٦)

Ma'ana: "Kuma kada ku aske kawunanku, har sai Hadaya ta kai wurinta". (Bakara 196)

Yanke farcen hannu ko na kafa zai shiga cikin wannan hukunci .

- Shafa turare a jiki, ko a tufafi ko a cikin abinci, saboda Hadisin wanda ya fado daga kan abin hawansa a wurin hajji (ya mutu) Manzon Allah

(S.A.W) ya ce: "Kada ku sanya masa turare, kuma kada ku rufe kansa"

Baya halatta ga wanda yake cikin kayan harami ya sanya wani tufafi wanda aka shafa wa kowane nau'i na turare, ko za'faran

- Saduwa da mace, (wato jima'i), yana daga cikin manyan abubuwan da ke bata hajji, ko umrah, yana bata hajji kafin tahallulin farko (wato jifa da saisaye a ranar goma ga wata), kuma dole mutum ya karasa wannan aikin hajjin, sa'an nan idan shekara ta zagayo ya sake wani, kuma ya yanka rakumi. Hakanan duk wata harka ta biyan bukatar sha'awarsa da mace bata halatta a gare shi ba, wannan ya hada da sumba da duka sauran wasannin da basu kai jima'i ba.
- Ya haramta a gare shi, ya daura ma wani aure, ko a daura masa. Saboda fadin Manzon Allah (S.A.W): "Wanda ya shiga cikin Ihrami, to baya halatta a gare shi ya aura, ko ya aurar, ko ya nemi aure".

- Ya haramta ga namiji ya sanya duk wani abu dinkakke, kamar riga, ko 'yar ciki (singileti) ko wando. Kuma ba ya halatta ga namiji ya rufe kansa, da hula, ko rawani da makamantansu.
- Ya haramta ga Alhaji, mace ko namiji ya yi farauta, ko ya temaka wurin farautar, ko ya kori abin farautar daga wurin da yake.
- Ba ya halatta ga mace (a wurin aikin hajji ko umrah) ta rufe fuska da Nikabi (wato mayanin da a ke dinka shi yana rufe dukkanin fuska, face ramun idanu guda biyu kawai), ba a ganin komai sai idonta. kuma ba ya halatta, ta sanya safar hannu. Saboda fadin Manzon Allah (S.A.W): "Kada mace wadda tayi harami ta sanya Nikabi ko Safar hannu." amma zata iya rufe fuskarta (da abin da ba nikabi ba) idan da wasu maza a wurin, saboda fadar A'isha (R.A): "Mazaje (mahaya) sun kance suna wuce mu, muna tare da Manzon Allah (S.A.W) idan sun matso kusa da mu, sai mu rufe fuskokinmu da karin da ke jikin abayarmu

ta warin kawunanmu), idan sun wuce sai mu bude "

3. Ka yawaita Talbiyya har sai ka isa Makka, ka fara kewaye Ka'aba. Idan ka isa Ka'aba, to kayi Dawafi sau bakwai (dakin Ka'aba yana hannunka na hagu) ka fara daga saitin "HAJARUL ASWAD" kuma za ka kare ta wurin da ka fara. Sa'an nan kayi salla raka'a biyu a bayan "MAKAMU IBRAHIM" idan ka sami wuri, idan babu wuri, to kayi a ko'ina.

4. Idan ka gama sallar, sai ka tafi zuwa dutsen "SAFA", ka fara Sa'ayi a tsakanin "SAFA" da "MARWA", za ka yi Sa'ayin ne sau bakwai, ka fara da "SAFA" ka kare da "MARWA". (abin nufi shi ne, daga "SAFA" idan ka tafi "MARWA" ka yi daya kenan, idan ka dawo "SAFA" ka yi biyu, haka za ka yi har sau bakwai) ka fara da "SAFA" ka kare da "MARWA".

5. Idan ka kare Sa'ayi, sai ka aske gashin kanka, ko ka yi saisaye, amma askewa gaba daya ya fi lada. Idan ka gama wannan, to ka

gama umrah kenan, sai ka cire kayan Ihrami, ka sanya kayanka na yau da kullum.

6. Idan hajji za ka yi kawai, banda umrah (wato Ifradi) to, idan ka zo mikati sai ka ce: "لبيك حجا" LABBAIKA HAJJAN bayan haka sai ka yawaita Talbiyya, har sai ka jefi JAMRATUL AQABA (Babban shaidan, ranar goma ga wata) idan ka isa Ka'aba sai ka yi Dawafin isowa sau bakwai, idan ka so sai ka gabatar da Sa'ayi tsakanin "SAFA" da "MARWA", ta yadda idan ka zo yin Dawafin Ifala ba sai ka yi Sa'ayi ba. Hakanan ba za ka aske kanka ba, kuma ba za ka cire Ihraminka ba, har sai ranar salla.

7. Idan za ka hada tsakanin hajji da umrah (wato Kirani) to sai ka ce (lokacin da za ka shiga harami):

"لبيك عمرة وحجا" LABBAIKA UMRATAN WA HAJJAN.

Sa'an nan ka yawaita Talbiyya, har sai ka jefi "JAMRATUL AQABA" (Babban shaidan), ka yi kamar yadda mai Ifradi yake yi.

**AIKIN HAJJI:**

1. Ranar takwas ga wata zul Hijja, ka yi Ihrami da hajji daga gidan da ka sauka (a Makka) -idan kana tamattu'i ne- ka yi wanka idan ka sami dama, sa'an nan ka sanya kayan Ihrami, sai ka ce: لبيك حجا LABBAIKA HAJJAN. Daga nan za ka yawaita Talbiyya har sai ka jefi "JAMRATUL AQABA" (Babban shaidan)

2. Amma idan "Kirani" ko "Ifradi" kake yi, to ihramin farko ya ishe ka (za ka bar kayan Ihramin a jikinka ba za ka cire ba).

3. Daga nan, za ka fita zuwa Mina, idan ka isa sai ka yi sallar Azuhur raka'a biyu la'asar biyu, magariba uku, Isha'i ita ma raka'a biyu, subahi raka'a biyu. Kowace salla za ka yi ta a kan lokacinta (ba za ka hada ba)

4. Idan rana ta fito, ta ranar tara ga wata (ranar Arfa) za ka tafi zuwa filin Arfa, kana mai Talbiyya, idan ka isa za ka yi sallar Azuhur da La'asar raka'a bibbiyu, a lokacin sallar Azuhur, za a kira salla sau daya a tada Ikama sau biyu (kowace

salla da ikamarta) za ka tsaya a Arfa, har sai rana ta fadi, a tsayuwarka ka yawaita addu'a da ambaton Allah, kana mai fuskantar Alkibla.

Dan'uwana ka tabbata ka shiga cikin filin Arfa, kar ka sake ka fita har sai rana ta fadi.

5. Idan ka tabbata rana ta fadi, to sai ka tafi zuwa Muzdalifa cikin natsuwa banda turereniya, idan ka isa can, sai ka yi sallar Magariba da Isha'i tare, kiran salla sau daya, Ikama sau biyu, Magariba raka'a uku, Isha'i raka'a biyu. Idan kayi sallar Subahi, ka zauna har rana ta kusa fitowa.

6. Idan rana ta kusa fitowa, sai ka kama hanyar Mina kana mai Talbiyya, idan ka isa Mina, za ka yi ayyuka kamar haka:

- Za ka jefi "JAMRATUL AQABA" (Babban shaidan), ita ce Jamra ta karshe, a kan hanyarka ta zuwa Makka, daga Mina, za ka i jefe ta, da tsakonkoni bakwai, daya bayan daya, kana mai kabbara (ALLAHU AKBAR) yayin jefa kowace tsakuwa, ka yi kokari tsakuwarka ta fada ramin Jamra.

- Sai ka yanka Hadayarka, ka ci daga cikinta, kuma ka yi sadaka da saura. Wanda ya yi "Tamattu'i" ko "Kirani", dole ne ya yi Hadaya, Idan ba shi da hali, to sai ya yi azumi guda uku, a lokacin aikin hajji, guda bakwai idan ya koma gida.
- Sai ka aske kanka gaba daya, ko ka yi saisaye, amma kwalkwali ya fi lada. Amma mace ta na yanke kamar tsawon gabar karshe ne ta yatsun hannunta, (ko kamar tsawon farcen hannunta). Za ka yi wadannan abubuwa kamar yadda aka jera, za ka fara jifa, sai yanka, sa'an nan aski. Amma idan ka gabatar da wani a kan wani, to babu laifi, idan ka gama wadannan abubuwa uku, sai ka sanya kayanka na yau da kullum, (wannan shi ne ake ce wa Tahallulin farko) duk abin da ya haramta a gareka da farko, to ya halatta, amma banda mata (jima'i).

7. Daga nan, sai ka tafi Makka domin Dawafin Ifala, wato Dawafin Hajji, bayan haka sai ka yi Sa'ayi a tsakanin "SAFA" da "MARWA" Sa'ayin hajji, idan Tamattu'i kake yi. da wannan za ka kasance ka yi Tahalluli na biyu, kome ya halatta gare ka hatta mata (jima'i).

8. Amma idan Ifradi ko Kirani kake yi, sai ka yi Dawafi kawai, ka yi Sa'ayi idan baka yi a farko ba.

9. Idan ka gama sai ka bar Makka, ka tafi Mina ka kwana biyu, (sha daya da sha biyu ga zul hajji).

10. A zamanka na Mina (sha daya da sha biyu) za ka jefi Jamrori guda uku, bayan rana ta yi zawali, za ka fara da Jamrar farko (shaidan karami, wadda take kusa da Mina ta fi nisa da Makka). Sa'an nan sai ta tsakiya, (shaidan na tsakiya) daga nan sai "JAMRATUL AQABA" (Babban shaidan). Za ka jefi kowace Jamra da tsakonkoni bakwai, daya bayan daya, kayi kabbara (ALLAHU AKBAR) yayin jefa kowace tsakuwa. Ana son bayan ka gama jifan Jamra ta

farko, da ta biyu, ka tsaya ka yi addu'a, kana mai fuskantar Alkibla. Jifan da wasu suke yi kafin zawali bai yi ba.

11. Idan ka gama jifa ranar sha biyu, idan ka so ka yi gaggawa ka fita kafin faduwar rana, to babu laifi, idan kaso ka jinkirta har sha uku, to hakan yafi, amma za ka yi jifa, a ranar sha uku kamar sauran kwanakin da suka wuce.

12. Idan za ka bar Makka zuwa garinku to sai ka yi Dawafin ban kwana (shi ma kewaye bakwai), amma mace mai jinin al'ada ko na biki ba sai ta yi ba.

## ZIYZARAR MADINAR MANZON ALLAH (S.A.W):

Dan'uwa ka sani cewa ziyarar Masallacin Manzon Allah (S.A.W) mustahabbi ce ga kowane Musulmi a lokacin hajji, ko ba lokacin hajji ba. Saboda fadin Manzon Allah (S.A.W): "Ba a daura sirdi, domin ziyarar wani masallaci sai masallatai

uku, masallacin Makka, da na Madina da na Kudus."

Idan ka isa Madina –cikin tsarewar Allah da kiyayewarsa- to sai ka fara da masallaci, domin salla a cikinsa ta fi salla dubu a waninsa. Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: "Salla a masallacina ta fi salla dubu a waninsa, sai dai idan masallacin Makka ne."

Idan ka gama sallar, sai ka tafi ka yi sallama ga Manzon Allah (S.A.W) tare da abokansa biyu, Abubakar da Umar (R.A) a dakin da kaburburansu suke.

Ana son ka ziyarci Masallacin Kuba, saboda fadin Manzon Allah (S.A.W): "Duk wanda ya fita zuwa Masallacin Kuba ya yi salla a cikinsa yana da ladan mai Umra."

Kuma za ka iya ziyarar Baki'a, da shahidan Uhudu ka yi musu addu'a, kuma ka nema musu gafara, kamar yadda Manzon Allah (S.A.W) yake yi. Idan ya je yana yi musu addu'a kamar haka

"السلام علي أهل الديار من المؤمنين والمسلمين وإنا إن شاء الله بكم للاحقون

ASSALAMU 'ALA AHLID DIYARI MINAL MU'MININA WAL MUSLIMINA, WA INNA INSHA'AL LAHU BIKUM LALAHIKUNA.

Ma'ana: "Amincin Allah ya tabbata a gare ku, ku ma'abota wadannan gidaje (kaburbura) daga cikin muminai da musulmai, lalle mu ma muna nan tafe bayanku in Allah ya yarda."

Ya dan'uwa -Allah ya kare ka daga duk wani mugun abu- wadannan wurare kawai ake ziyarta a Madina, amma sauran wuraren babu wanda ya sa ka ka ziyarce su, balle ka yi salla a wurin. Da akwai wani alheri a ziyarar wuraren da Manzon Allah (S.A.W) ya yi mana bayani, domin shi ne Annabinmu, kuma masoyinmu, kuma yana son mu da alheri. Kuma dukkan mu mun tabbata ya isar da sakon da Allah ya aiko shi da shi, kuma ya bayar da amanar da aka ba shi, ya yi wa al'umma nasiha, ya bar mu a kan wata hanya fara sosai, darenta kamar rana yake (wurin haske), babu

wanda zai karkace daga gare ta, sai hallakakke. Allah bai karbi ransa ba, har sai da ya cika addini da shi, kuma ya cika wa al'umma ni'ama da shi. Ya Allah kayi dadin tsira da aminci a gare shi, tare da mutanen gidansa da sahabbansa baki daya.

**SAKO NA BIYU**

Dan'uwana Alhaji akwai wasu kura-kurai, da Alhazai suke fadawa ciki, imma saboda jahilci, ko mantuwa, ko kuma halin ko-in-kula.

A nan zan ambaci wasu daga ciki, domin ka guje su, ko hajjinka ya zama karbabbe da ikon Allah.

**NA FARKO:**

Kura-kurai da wasu suke yi wurin Ihrami:

- Barin Ihrami daga Mikati.
- Wasu suna zaton ba ya halatta su sa silifas matukar ba da shi suka yi Ihrami ba.

- Wasu Alhazai suna zaton ba ya halatta su canza kayan da suka yi Ihrami da su, abin da ya inganta shi ne cewa: Alhaji yana da damar ya canza kayan Ihrami duk lokacin da ya ga dama.
- Fitar da kafadar dama, wurin sanya kayan Ihrami. ba a fitar da kafada Idan an sanya Ihrami sai wuri daya kawai, shi ne wurin Dawafin isowa (Dawafin farko da mutum zai yi farkon shigan shi Makka).
- Zaton wasu, cewa akwai wata salla wajiba, ta musamman da a ke yi wurin yin Ihrami.

**NA BIYU:**

Kura-kurai da wasu mutane suke yi, daga mikati zuwa masallacin Makka

- Barin Talbiyyah da shagaltuwa da wasu maganganu, ko abin da yafi magana hadari, kamar sauraron kide-kide.
- Yin Talbiyya da sauti daya (ko wani yana yi suna amsawa)

**NA UKU:**

Kura-kurai wurin shiga masallacin Makka:

- Jin cewa wajibi ne sai mutum ya shiga ta wata kofa ta daban, sai ka ga wasu suna wahalar da kawunansu wurin nemar "BABUL UMRAH" ko "BABUL FATH" ko wasu ba wadannan ba, Alhamdullil lahi, duk abin bai kai haka ba, ka shiga ta kowace kofa kake so, idan ka shiga ta "BABU BANI SHAIBA" (wato Babus Salam, a yanzu), to hakan ya yi kyau, saboda ya zo cikin Hadisi cewa Manzon Allah (S.A.W) ya shiga ta nan.

- Kebance wata addu'a ta musamman wurin shiga Harami , ba a samo wani du'a'i na musamman da ake shiga Harami da shi ba, du'a'in da aka samo daga Manzon Allah (S.A.W), domin shiga kowane masallaci da shi, wanda daga ciki har da Harami shi ne:

بسم الله والصلاة والسلام علي رسول الله، رب اغفر لي ذنوبي وافتح لي أبواب رحمتك.

BISMILLAHI WASSALATU WASSALAMU 'ALA RASULIL LAHI, RABBIG FIRLI DHUNUBI WAFTAH LI ABWABA RAHMATIKA.

Ma'ana: "Ina shiga masallaci da sunan Allah, Allah ka yi dadin tsira da aminci ga Manzon Allah, Ya Ubangiji ka gafarta mun zunubaina, kuma ka bude mini kofofin rahamarka.

**NA HUDU:**

Kura-kurai wurin Dawafi:

- Furta niyya wurin fara Dawafi, za ka ji wasu suna cewa: "Ya Allah nayi niyyar

yin Dawafi zagaye bakwai". Wannan addu'a ba a samu Manzon Allah (S.A.W) yana yin ta ba, ko Sahabbansa masu girma, za ka yi niyya a cikin zuciyarka ne.(ba tare da furtawa ba)

- Wasu ba su fara Dawafi daga saitin "HAJARUL ASWAD". Duk wanda ya fara Dawafi ba daga saitin "HAJRUL ASWAD" ba, to wannan zagayen bai yi ba.
- Turereniya da mutane suke yi wurin sumbantar "HAJARUL ASWAD" ko taba "RUKUNUL YAMANI". tutture mutane ko cutar da su baya halatta.
- Jin cewa sumbantar "HAJARUL ASWAD" sharadi ne da Dawafi baya inganta sai da shi. Abin da shari'a ta zo da shi shi ne: ka sumbanta idan ka sami dama.
- Sumbantar "RUKUNUL YAMANI" (wasu suke yi)

- Sassarfa a kowane zagayen Dawafi. Abin da sunnah takarantar da mu shi ne: Za ka yi sassarfa a gewayen farko zuwa na uku, ka yi tafiya a sauran hudu, wannan ya shafi maza kawai (amma mata tafiya za su yi a duka)
- Kebance kowane zagaye da addu'a ta musamman. Bidi'ar ta kan kara girmama ne yayin da za ka ga wasu sun dauki wani littafi suna karantawa, amma basu san abin da suke fadi ba.
- Shiga ta cikin "HIJRU ISMA'IL" yayin Dawafi. idan mutum ya yi haka to Dawafinsa ya baci, saboda "HIJRU ISMA'IL" cikin Ka'aba yake.
- Rashin sanya Ka'aba a hagu, musamman yadda masu tafiya tare da mata suke yi. Za ka ga sun kama hannun juna (suna tafe suna kakkare su) wanda wannan zai ja mutum ya sanya Ka'aba a damanshi, ko gabanshi,

ko bayanshi. Wannan zai iya bata mishi Dawafi! Saboda sa Ka'aba a hagu yana cikin sharuddan ingancin Dawafi.

- Shafan Rukunnan Ka'aba duka.
- Daga sauti wurin addu'a, wanda yin hakan yana tafiyar da natsuwa. Kuma yana rage wa Ka'aba kwarjini, kuma ya ruda sauran mutane da suke Dawafi, ga shi ruda mutum idan yana ibada babu kyau.
- Zaton cewa raka'a biyu da ake yi bayan gama Dawafi ba su yi, idan ba a kusa da "MAKAMU IBRAHIM" aka yi ba. Sai ka ga mutum yana marmatse mutane suna Dawafi. Yin haka cutarwa ce mai yawa.
- Tsawaita sallar bayan Dawafi. Yin haka ya saba wa sunna, saboda Manzon Allah (S.A.W) ya kasance yana sassauta ta, kuma idan ka tsawaita za ka cutar da masu Dawafi, kuma ka

matsa wa wadanda suka fi ka cancantar wurin.

- Kebance "MAKAMU IBRAHIM" da du'a'i na musamman. Bidi'ar takan karu, yayin da suka zama suna yi da sauti daya.
- Shafar "MAKAMU IBRAHIM" wanda ba a samu Manzon Allah (S.A.W) yana hakan ba.

**NA BIYAR:**

Kura-kurai wurin "SAFA" da "MARWA":

- Furta niyya. Ita niyya mahallinta zuciya. Ba a furta ta.
- (Wasu mazan suna) barin sassarfa a tsakanin alamomi biyu koraye.
- Ko akasin wanda ya gabata, za ka ga wasu suna gudu a Sa'ayi duka. Hakan yana jan musu matsaloli kamar haka:

1. Saba wa sunnar Manzon Allah (S.A.W)

2. Ya wahalar da kansa.

3. Tutture mutane da matsarsu, wani yana sauri ne, don ya gama Ibadar, hakan kuwa sharri ne, saboda hakan yana fassara cewa ya gaji da ibadar kenan (yana kokari ya gama). Ya kamata a ce ya yi bautar cikin dadin rai da farin ciki da natsuwa.

- Karanta Ayar: "إن الصفا والمروة"

A kowane hawa kan dutsen "SAFA" ko "MARWA" Abin da ya zo daga Manzon Allah (S.A.W) shi ne: karanta wannan aya a lokacin hawa "SAFA" na farko yayin fara Sa'ayi. Manzon Allah (S.A.W) ya karanta ayar ne domin ya labarta abin da Allah ya fara fada a cikin Alku'ani domin shima ya fara da shi, shi ne:

أبدأ بما بدأ الله به: إن الصفا والمروة من شعائر الله فمن حج البيت أو اعتمر فلا جناح عليه أن يطوف بهما ومن يطوع خيرا إن الله شاكر عليم.

ABDA'U BIMA BADA'AL LAHU BIHI: INNAS SAFA WALMARWATA MIN SHA'A'IRIL LAHI,

FAMAN HAJJAL BAITA AWI'TAMARA FALA JUNAHA 'ALAIHI ANYATTAWAFA BIHIMA, WAMAN TATAWWA'A KHAIRAN FA'INNAL LAHA SHAKIRUN 'ALIM.

Ma'ana: "Ina farawa da abin da Allah ya fara da shi: "lalle ne Safa da Marwa suna daga wuraren bautar Allah, to wanda ya yi hajjin Daki ko kuwa ya yi umrah, to babu laifi a kansa da ya gewaye su, su biyu. Duk wanda ya kara yin wani aikin alheri, to lalle ne Allah mai godiya ne, Masani."

- Kebance kowane zagaye da addu'a ta musamman.
- Fara Sa'ayi daga "MARWA"
- Zaton cewa sai ka dawo "SAFA" daga "MARWA" sannan ka yi daya. (abin nufi shi ne, mutum ya fara Sa'ayi daga "SAFA" idan ya kai "MARWA" sai ya ce nayi rabi kenan idan ya dawo "SAFA" sai ya ce daya kenan) zai yi Sa'ayi sau goma sha hudu kenan, a maimakon bakwai.

- Yin Sa'ayi na nafila kamar Dawafi, kamar yadda wasu suke zaton cewa ya halatta ka yi hakan.

**NA SHIDA:**

Kura-kurai wurin aski:

- Aske wani sashe na kai, da barin wani.
- Diban gashin kai dan kadan daga gefe daya, wannan ya saba wa maganar Allah da sunnar ManzonSa (S.A.W) Allah yana cewa: "محلقين رؤوسكم ومقصرين"

Ma'ana: kuma masu aske kawunanku da masu saisaye.

- Yin aski bayan ya cire Ihrami, ya sa kayansa na yau da kullum, a umra (aski a ke farawa sa'annan a cire Ihrami)

**NA BAKWAI:**

Kura-kurai da ke faruwa ranar Tarwiyya (takwas ga watan zul hijja)

- Zaton cewa ya wajaba mutum ya sallaci raka'a biyu, bayan ya sa Ihrami, ko zaton cewa wajibi ne mutum ya sanya Ihrami sabo.
- Fitar da kafada yayin da aka sa Ihrami. A wuri daya ake fitar da kafada, (kamar yadda ya gabata) wurin Dawafin isowa kawai (wato Dawafin da za ka yi farkon shiganka Makka).
- Zaton cewa baya halatta mutum ya sa Ihramin da ya yi umrah da shi.
- Rashin bayyana talbiyya a kan hanya zuwa Mina.
- Tafiya Arfa kai tsaye. (a ranar takwas ga wata)
- Kin tafiya Mina da zama a Makka.
- Hada salloli biyu a Mina (kamar Azuhur da La'asar).
- Cika salla a Mina (wato rashin yin kasaru).

**NA TAKWAS:**

Kura-kurai da suke faruwa a Arfa:

- Kin bayyana Talbiyya a lokacin fita Arfa.
- Tsayuwa ba a Arfa ba, bayan rana ta yi zawali.
- Fuskantar dutsen Arfa wurin addu'a ba alkibla ba.
- Zaton wajabcin tsayuwa kusa da Dutsen.
- Zaton cewa filin Arfa yana cikin Harami ne, saboda haka ba ya halatta a yanke Itatuwansa.
- Jin cewa dutsen yana da wata daraja ta musamman. Sai ka ga wasu sun hau kansa suna salla, ko suna rataya wasu abubuwa a kan itatuwansa.
- Fita daga filin Arfa kafin rana ta fadi.
- Bata lokuta a filin Arfa, ba tare da wata fa'ida ba. Laifin yana kara girma yayin

da za a bata lokutan wurin abubuwa marasa amfani, kamar daukan hoto, da sauraron kide-kide da wake-wake, batsa, da yi da mutane.

**NA TARA:**

Kura-kurai da suke faruwa a kan hanyar Muzdalifa:

- Yin sauri da yawa.
- Sauka kafin a kawo Muzdalifa.
- Sallar Magariba da isha'i kafin a sauka a Muzdalifa.
- Jinkirta sallar isha'i har lokacinta ya fita, da hujjar cewa ba' a isa Muzdalifa ba. Wasu Alhazai idan mota ta jinkirta su a hanya, sai su ki yin salla, har dare ya kai rabi, ko kusa da fitowar alfijir, ba su yi salla ba, wai sai sun kawo Muzdalifa. Yin haka kuskure ne mai girma, abin da ya zama wajibi akansu shi ne: su yi

salla duk inda suke idan sun ji tsoron fitar lokacinta.

- Yin sallar asuba kafin lokacinta ya shiga, wasu basa kulawa da lokacin fitowar alfijir, da jin wani ya kwala kiran salla, sai su yi wuf su tashi su yi salla (kafin lokacinta ya shiga)
- Wasu suna fita Muzdalifa da dare. ba su kwana a cikinta.
- Kashe dare da wasu suke yi, da jita-jita, ko da wasu abubuwa da suka haramta.
- Wasu suna zama a Muzdalifa har sai rana ta fito.
- Zaton cewa wajibi ne a tsinci duwatsu a Muzdalifa.

**NA GOMA:**

Kura-kurai wurin jifa:

Hakika Manzon Allah (S.A.W) ya bayyana hikimar dake cikin jifa, lokacin da yake cewa: "Ba a sha'anta Dawafi ga Ka'aba, da Sa'ayi a tskanin

"SAFA" da "MARWA" da Jifa ba, face sai don a wanzar da ambaton Allah."

Daga cikin kura-kurai da suke faruwa wurin jifa:

- Wanke tsakonkonin, ko kuma sanya musu turare.
- Zaton wadannan abin jifa shaidanu ne. To ba haka ba ne, ana jifa ne domin wanzar da ambaton Allah, kuma a cika bautar Allah Madaukakin Sarki.

Dalilin wannan zato za ka ga mutane suna fadawa kura-kurai kamar haka:

1. Za ka ga wani ya taho da fushi, da bacin rai (wai shi zai jefi shaidan) hakan ya ja shi zuwa ga cutar da muta ne.

2. A maimakon mutum ya hararo cewa bautar Allah yake yi, da wannan jifa, sai ka ga yana canzawa, a maimakon ya ambaci Allah da abin da ya zo a shari'a, sai ka ga yana ambaton Allah da abin da bai zo a shari'a ba, hakan na faruwa ne saboda wannan zaton. Sai ka sami mutum ya

dauki duwatsu manya, da sanduna da takalma (wai shi zai jefi shaidan.)

- Wasu suna zaton cewa sai tsakuwar ta sami wannan ginshiki, a'a, idan ta fada wannan ramin ma ya isa.
- Wakilta wani ya yi masa jifa, alhali zai iya zuwa da kansa ya yi.
- Zaton cewa ba ya halatta a yi jifa sai da tsakonkonin Muzdalifa. Ingantacciyar Magana ita ce: ya halatta ayi jifa da kowace tsakuwa kuma ko ta ina ce.
- Rashin yin jifan a jere, ko farawa da wurin jifa na karshe karshe.
- Yin jifa kafin lokaci ya shiga.
- Jifa da tsakonkonin da ba su kai bakwai ba.
- Rashin yin addu'a bayan gama jifan farko da na biyu.
- Kari wurin adadin tsakonkoni, ko adadin wurin jifa.

**NA GOMA SHA DAYA:**

Kura-kurai a Mina:

- Kin kwana a Mina ba tare da uzuri ba, wasu suna kin kwana a Mina ne, da hujjar cewa ba su samu wuri ba, alhali ba su duba sosai ba ne, sai su tafi Makka ko Aziziyya su kwana.
- Fita daga Mina kafin rana ta yi zawali, ranar sha biyu ga wata .

Abu na karshe, ka sani ya kai dan'uwa Alhaji, akwai wasu mutane da basa kula da irin kudin da zasu yi hajji da shi, sai ka samu suna hajji da kudin haramun! Sun manta cewa shi Allah Mai tsarki ne, ba ya karban wani aiki sai mai tsarki .

Wadansu su kuma idan sun gama aikin hajji sai ka ga suna saya wa iyalansu tsaraba ta haramun, kamar kaset din wake-wake da kide-kide, da kuma abubuwa na shagala, da manta Allah. Idan mutum ya yi haka, to bai gode ni'imar

Allah da ya yi mishi ba, kuma ana ji wa mutum tsoro, idan ya yi haka a ki karbar hajjinsa.

Dan'uwana Alhaji, ka yi kokari ka ga ka yi hajji da kudi na halas, kuma ka saya wa iyalanka da yaranka abin da zai amfane su, kamar littattafai masu kyau da kasussuka masu ma'ana.

**SAKO NA UKU**

Ka sani ya kai dan'uwa mai girma –Allah ya kare ka daga kowane shirri da zunubi- Shaidan yana bakin kokarinsa, wurin sai ya ga ya batar da Musulmi, ta hanyar kawata musu sharri a cikin zukatansu, Allah ya ba mu labarin Shaidan inda ya ce:

"وقال لأتخذن من عبادك نصيبا مفروضا"(النساء ١١٨)

Ma'ana: "Kuma ya ce: lalle ne, zan rika rabo yankakke daga bayinka. (Nisa'i 118).

Allah ya sake ba mu labarinsa, lokacin da ya ce:

قال فبما أغويتني لأقعدن لهم صراطك المستقيم ثم لآتينهم من بين أيديهم ومن خلفهم وعن أيمانهم وعن شمائلهم ولا تجد أكثرهم شاكرين (الأعراف ١٦-١٧)

Ma'ana: ya ce:" To ina rantsuwa da hallakawar da ka yi mini, lalle ne zan zauna musu kan hanyarka madaidaiciya, sa'an nan hakika ina mai je musu ta gaba gare su, da kuma baya gare su, kuma zan je musu ta damansu, da barin hagunsu, kuma ba za ka sami mafi yawansu masu godiya ba." (A'araf16-17)

Kuma Allah ya hana mu bin hanyoyin shaidan inda yake cewa:

يأيها الذين ءامنوا لا تتبعوا خطوات الشيطان ومن يتبع خطوات الشيطان إنه يأمر بالفحشاء والمنكر ولولا فضل الله عليكم ورحمته ما زكى منكم من أحد أبدا ولكن الله يزكي من يشاء والله سميع عليم(النور ٢١)

Ma'ana: "Ya ku wadanda suka yi imani, kada ku bi hanyoyin shaidan, kuma wanda ke bin hanyoyin shaidan, to lalle shi yana umurni da yin alfasha da abin da ba a sani ba (wato abin da a ke kyamarsa), kuma ba domin falalar Allah ba, a

kanku da rahmarSa babu wani mutum daga gare ku da zai tsarkaka har abada, kuma amma Allah yana tsarkake wanda yake so, kuma Allah mai ji ne Masani. (Nur 21)

Abu mafi hadari da Shaidan yake jefa dan'adam a ciki shi ne shirka da Allah! don ya sani cewa Allah baya gafarta shi. Allah ya na cewa:

إن الله لا يغفر أن يشرك به ويغفر ما دون ذلك لمن يشاء (النساء ٤٨)

Ma'ana: "lalle ne Allah ba ya gafarta a yi shirka game da shi, kuma yana gafarta abin da yake bayan wannan ga wanda yake so. (Nisa'i 48)

Kuma ka sani cewa Shaidan ba ba sai ya umurce ka da ka yi shirka kai tsaye ba, a a zai umurce ka ne da wasu abubuwa wadanda daga karshe za ka fada shirka tsundum saboda su.

Mutanen Annabi Nuhu (a.s) su suka fara shirka a bayan kasa. akwai wasu mutanen kwarai da suka mutu, sai shaidan ya kawata musu cewa su

yi gumakansu, su aje a wurin da suke zama, ko sa samu karfin gwiwa wurin ibada (idan suna kallon gumakansu suna tunawa da su) lokacin da wadan nan suka mutu, wasu suka zo bayansu, sai shaidan ya ce musu: "lalle iyayenku basu kafa wadannan gumaka ba face sai su rinka neman taimakonsu, idan musiba ta sauka a kansu". Bai gushe ba yana kokari har sai da ya ga sun bauta wa wadannan gumaka ba Allah ba.

Jahilci yana sa wasu mutane fadawa cikin wasu abubuwa da za su iya kaiwa ga shirka, amma basu sani ba, kamar fadin wasu: Ya Alhusain, ko Ya sitti zainab, ko Ya Badawi, Ya mutawalli, ko Ya shugabana wane, ko (fadin wasu): Ina neman tsarinka kuma ina neman taimakonka ka warkar mun da mara lafiyana (wane) ko ka dawo min da matafiyina gida lafiya, ko ka bani yaro, ko ka taimake ni a kan makiyina, ko wanda ya zalunce ni.

Yana daga cikin shirka, sujada ga kabari, ko salla a fuskanci kabari, har wasu suna zaton ya fi

a kalli alkibla lada, ko jin cewa Dawafi ga kabari ya fi Dawafi ga Ka'aba.

Ya dan'wana! ba wanda bai san cewa wadannan abubuwa shirka ne ba, kana ganin mutum mai hankali, zai nemi temakon wanda ya mutu? Da zai iya temakon kansa da bai mutu ba. Wanda ake kira ya kai Manzon Allah ne? Wanda babu kamarsa a duniya, amma duk da hakan Allah ya umurce shi ya fada wa mutane cewa:

قل لا أملك لنفسي نفعا ولا ضرا إلا ما شاء الله ولو كنت أعلم الغيب لاستكثرت من الخير وما مسني السوء إن أنا إلا نذير وبشير لقوم يؤمنون(الأعراف ١٨٨)

Ma'ana: "Ka ce ba ni mallaka wa raina wani amfani, kuma haka ban tunkude wata cuta, face abin da Allah yaso, kuma da na kasance ina sanin gaibi, da lalle ne na yawaita alheri a rayuwata, da kuma wani mugun abu bai same ni ba, ni ban zama ba face mai gargadi, da kuma yin bishara ga mutane wadanda suke yin imani. (A'araf 188)

Kuma Allah ya sake cewa:

قل إني لا أملك لكم ضرا ولا رشدا قل إني لن يجيرني من الله أحد ولن أجد من دونه ملتحدا (الجن ٢١-٢٢)

Ma'ana: "Ka ce: lalle ne, ni ba ni mallakar wata cuta gare ku, kuma ba ni mallakar wani alheri, ka ce: lalle ne, ni kowa baya iya cetona daga Allah, kuma ba zan iya samun mafaka daga gare shi ba. (Jin 21-22)

Idan Manzon Allah (S.A.W) ba ya iya mallaka wa kansa wani alheri ko wata cuta, kuma ba wanda ya isa ya cece shi daga Allah (idan ya yi nufin cutar da shi) to Musulmi ya yi zaton wani daban zai iya mallaka masa alheri ko sharri? Babu Musulmin kwarai da zai yi wannan zaton. Allah madaukaki ya sake cewa:

ويعبدون من دون الله ما لا يضرهم ولا ينفعهم ويقولون هؤلاء شفعاؤنا عند الله قل أتنبئون الله بما لا يعلم (يونس ١٨)

Ma'ana:"Kuma suna bauta wa wanda ba Allah ba, abin da ba ya cutar da su kuma ba ya amfanar da su, kuma suna cewa wadannan ne masu cetonmu a wurin Allah, to ka ce: shin kuna

bai wa Allah labarin abin da bai sani ba? (Yunus 18)

Wannan shi ne aikin mushrikai tare da gumakansu, yanzu ya kamata ga Musulmi ya kwaikwayi aikin mushrikai? Har ya nemi ceton wasu waliyyai bayan sun mutu?!!

Allah ya ba mu labarin mushrikai yayin da suke bauta wa gumakansu, suna cewa: ai bamu bauta musu face sai don su kusantar da mu zuwa ga Allah:

والذين اتخذوا من دونه أولياء ما نعبدهم إلا ليقربونا إلى الله زلفى إن الله يحكم بينهم في ما هم فيه يختلفون إن الله لا يهدي من هو كاذب كفار(الزمر٣)

Ma'ana: "Kuma wadanda suka riki wasu waliyyai ba Allah ba, suna cewa bamu bauta musu face domin su kusantar da mu zuwa ga Allah kusantar daraja, lalle Allah zai yi hukunci a tsakaninsu, ga abin da suka kasance suna sabawa a tsakaninsa. Lalle Allah ba ya shiryar da wanda ya kasance mai karya, mai yawan kafirci". (Zumar 3)

Shin za a iya samun Musulmi da ya yi imani da maganar Allah, sa'an nan ya kira wani waliyyi ba Allah ba, kuma ya kafa hujja da maganar mushrikai?

Allah ya bayyana raunin duk wanda ake kira ba shi ba, inda ya ce:

والذين يدعون من دونه لا يستطيعون نصركم ولا أنفسهم ينصرون (الأعراف ١٩٧)

Ma'ana: "Kuma duk wanda kuke kira ba Allah ba, ba su iya taimakon ku kuma basu iya taimaka wa kansu". (A'araf 197)

Idan Allah ya ce: lalle su ba su iya taimaka muku, kuma ba su iya taimakon kansu, to Musulmi mai hankali ya kamata ya gaskata cewa zasu iya taimakonsa ba Allah ba? Duk wanda ya fadi haka hakika ya karyata Allah, kuma duk wanda ya karyata Allah ya kafirta! Ko da yana salla yana azumi, kuma yana jin cewa shi Musulmi ne.

Ba ka ganin shugaban Annabawa, kuma shugaban duk wani dan'adam wanda a ka ba shi ceto ranar kiyama, duk mutane suna karkashin tutarsa, hatta Annabawa da Manzanni, saboda matsayi da darajar da Allah ya ba shi, amma duk da haka ba ya iya amfanar 'yan'uwanshi da wani abu, ka san abin da ya ce lokacin daya hau dutsen Safa? Bukhari ya ruwaito daga Ibnu Abbas da Abu Huraira suna cewa: "A lokacin da aka saukar wa Manzon Allah (S.A.W):

وأنذر عشيرتك الأقربين (الشعراء ٢١٤)

Ma'ana: "Kuma ka yi gargadi ga danginka mafiya kusanci." (Shu'ra'i 214)

Sai y ace : Ya ku taron Kuraishawa, ku fanshi kanku, ba zan iya amfanar da ku kome ba a wurin Allah, ya ku 'ya'yan Abdumanaf, ba zan iya amfanar da ku kome ba a wurin Allah, ya Abbas dan Abdulmuddalib, bazan iya amfanar da kai kome a wurin Allah ba, ya ke Safiyya goggon Manzon Allah, (S.A.W) bazan iya amfanar da ke wani abu ba a wurin Allah ba, ya ke Fadima diyar

Muhammad (S.A.W) tambaye ni abin da na mallaka daga dukiyata, ba zan iya amfanar da ke wani abu ba a wurin Allah.

Idan ba zai iya amfanar da dan'uwan mahaifinshi, da goggonshi, kai har dayarshi, kome ba, to wanda ba su ba, zai iya samun wani abu? Ka kula da wannan da kyau ya dan'uwana.

A lokacin da Manzon Allah (S.A.W) ya so ya nemi gafara ga Baffansa, Abu Dalib saboda shi ne ya raine shi, kuma ya temake shi, sai ubangiji ya hana shi, ya ce:

ما كان للنبي والذين ءامنوا أن يستغفروا للمشركين ولو كانوا أولي قربى من بعد ما تبين لهم أنهم أصحاب الجحيم (التوبة ١١٣)

Ma'ana: "Baya kamata ga Annabi ba da wadanda suka yi imani su bidi gafara ga mushrikai, ko da sun kasance ma'abota zumunta ne, bayan ya bayyana a gare su cewa lalle ne su ma'abota wutan jahim ne" (Tauba 113)

Lokacin Allah ya ga kwadayin ManzonSa ya yi yawa wurin ya ga Baffansa ya shiriya sai ya ce:

إنك لا تهدي من أحببت ولكن الله يهدي من يشاء وهو أعلم بالمهتدين (القصص ٥٦)

Ma'ana: "lalle ne kai ba ka shiyar da wanda kake so, sai dai shi Allah yana shiyar da wanda yake so, kuma shi ne yafi sani daga masu shiryarwa". (Kasas 56)

Ya dan'uwana mai girma, kada ka rudu da abin da wasu jahilai suke yi na kiran wani ba Allah ba, ka dogara ga rayayye wanda ba ya mutuwa, kar ka kira wani sai shi, kuma kar ka nemi mafaka sai a wurin Allah, kuma kar ka nemi temakon kowa sai na Allah, ka sani Allah yana kusa da kai fiye da kome. Allah yana cewa:

وإذا سألك عبادي عني فإني قريب أجيب دعوة الداع إذا دعان (البقرة ١٨٦)

Ma'ana: "Kuma idan bayina sunka tambaye ka game da ni, to lalle ni makusanci ne, ina amsa kiran mai kira idan ya kira ni." (Bakara 186)

Ya dan'uwana –Allah ya kiyaye ka- ka rike wasiyyar Manzon Allah (S.A.W) ga Abdullahi bni

Abbas, lokacin da ya ke gaya mishi: " Idan za ka yi roko, to ka roki Allah, kuma idan za ka nemi temako, to ka nemi temakon Allah, kuma ka sani da al'umma zata taru domin ta amfanar da kai wani abu, to baza ta iya amfanar da kai ba sai dai da abin da Allah ya rubuta cewa shi ne naka. Kuma da zasu taru don su cutar da kai da wani abu, to basu iya cutar da kai, sai dai abin da Allah ya rubuta zai same ka, (angama rubuta kome) kuma an dauke alkaluman, kuma takaddun da aka yi rubutun a kan su sun bushe.

Bana jin bayan wannan bayani, hujja ta rage ma wani. shin za a karbi maganar wani bayan maganar Allah da Manzonshi? Ina rokon Allah ya kare ka daga kowane mugun abu. akwai wasu addu'o'i masu girma, kuma masu amfani, Manzon Allah (S.A.W) ya kasance yana karantar da sahabbanshi su, ya kamata ka haddace su, kuma ka yi aiki da su:

اللهم إني أعوذ بك من جهد البلاء ودرك الشقاء وسوء القضاء وشماتة الأعداء

ALLAHUMMA INNI A'UDHU BIKA MIN JAHDIL BALA'I, WADARAKISH SHAQA'I, WASU'IL QADHA'I, WASHAMATATIL A'ADA'I.

Ma'ana: Ya Allah lalle ni ina neman tsarin ka daga mafi girman bala'i, da kuma tabewa, da mummunar kaddara, da kuma dariyar abokan gaba.

اللهم أصلح لي ديني الذي هو عصمة أمري وأصلح لي دنياي التي فيها معاشي وأصلح لي آخرتي التي فيها معادي واجعل الحياة زيادة لي في كل خير واجعل الموت راحة لي من كل شر

ALLAHUMMA ASLIH LI DINIYAL LADHI HUWA 'ISMATU AMRI, WA'ASLIH LI DUNYAYAL LATI FIHA MA'ASHI, WA ASLIH LI AKHIRATIYAL LATI FIHA MA'ADI, WAJ'ALIL HAYATA ZIYADATAL LI FI KULLI KHAIR, WAJ'ALIL MAUTA RAHATALLI MIN KULLI SHAR.

Ma'ana: Ya Allah ka kyautata mani addinina wanda shi ne marikin al'amurana, kuma ka gyara mani duniyata wadda a cikinta ne akwai rayuwata, kuma ka gyara mani lahirata wadda a cikin ta ne akwai makomata, kuma ka sanya

rayuwata ta zama karuwa a cikin kowane alheri, kuma ka sanya mutuwa ta zama hutu a gare ni daga kowane sharri.

اللهم إني أسألك من الخير كله عاجله وآجله ما علمت منه وما لم أعلم، وأعوذ بك من الشر كله عاجله وآجله ما علمت منه وما لم أعلم، اللهم إني أسألك من خير ما سألك منه عبدك ونبيك صلى الله عليه وسلم وأعوذ بك من شر ما استعاذ منه عبدك ونبيك صلى الله عليه وسلم اللهم إني أسألك الجنة وما قرب إليها من قول أوعمل وأعوذ بك من النار وما قرب إليها من قول أو عمل وأسألك أن تجعل كل قضاء قضيته لي خيرا.

ALLAHUMMA INNI AS'ALUKA MINAL KHAIRI KULLIHI 'AJILIHI WA AJILIHI, MA 'ALIMTU MINHU WAMALAM A'ALAM, WA'A'UDHU BIKA MINASH SHARRI KULLIHI, 'AJILIHI WA AJILHI, MA 'ALIMTU MINHU WAMA LAM A'ALAM, ALLAHUMMA INNI AS'ALUKA MIN KHAIRI MASA'ALAKA MINHU 'ABDUKA WA NABIYYUKA SALLAL LAHU ALAIHI WASALLAM, WA A'UDHU BIKA MIN SHARRI MAS TA'DHAKA MINHU 'ABDUKA WA NABIYYUKA SALAL LAHU 'ALAIHI WA SALLAM, ALLAHUMMA INNI AS'ALUKAL

JANNATA WAMA QARRABA ILAIHA MIN QAULIN AU 'AMAL, WA A'UDHU BIKA MINAN NARI WAMA QARRABA ILAIHA MIN QAULIN AU 'AMAL, WA AS'ALUKA ANTAJ'ALA KULLA QADA'IN QADAITAHU LI KHAIRAN.

Ma'ana: Ya Allah lalle ni ina rokonka dukkan alheri, na kusa da na nesa, wanda na sani da wanda ban sani ba, kuma ina neman tsarinka daga dukkan sharri na kusa da na nesa, wanda na sani da wanda ban sani ba. Kuma ina rokonka duk wani alheri, wanda Bawanka kuma Manzoka (S.A.W) ya rokeka, kuma ina neman tsarinka daga duk wani sharri wanda Bawanka kuma Manzonka (S.A.W) ya nemi tsarinka daga shi. Ya Allah lalle ni ina rokonka Aljanna da duk abin da zai kusantar dani zuwa gareta, na daga Magana ko aiki, kuma ina neman tsarinka daga wuta, da duk abin da zai kusantar dani zuwa gareta na daga Magana ko aiki. Kuma ina rokonka ka sanya duk wani hukunci da ka hukunta a kaina ya zama alheri.

اللهم احفظني بالإسلام قائما، واحفظني بالإسلام قاعدا، واحفظني بالإسلام راقدا ولا تشمت بي عدوا ولا حاسدا، اللهم إني أسألك كل خير خزائنه بيدك، وأعوذ بك من كل شر خزائنه بيدك.

ALLAHUMMAH FADHNI BIL'ISLAMI QA'IMAN, WAHFADHNI BIL'ISLAMI QA'IDAN WAHFADHNI BIL'ISLAMI RAQIDAN, WALA TUSHMIT BI 'ADUWWAN WALA HASIDAN. ALLAHUMMA INNI AS'LUKA KULLA KHAIRIN KHAZA'INUHU BIYADIKA, WA A'UDHU BIKA MIN KULLI SHARRIN KHAZA'INUHU BIYADIKA.

Ma'ana:Ya Allah ka barni cikin musulunci ina tsaye, kuma ka barni cikin musulunci ina zaune, kuma ka barni cikin musulunci ina kwance, kuma kar ka bari abokin gaba balle mai hassada ya yi mun dariya. Ya Allah lalle ne ni ina rokonka duk wani alheri, wanda taskokinsa suna hannunka, kuma ina neman tsarinka daga duk wani sharri wanda taskokinsa suna hannunka.

اللهم إني أسألك يا ألله بأنك الواحد الأحد الصمد الذي لم يلد ولم يولد ولم يكن له كفؤا أحد، أن تغفر لي ذنوبي إنك أنت الغفور الرحيم

ALLAHUMMA INNI AS'ALUKA YA ALLAHU, BI'ANNAKAL WAHIDUL AHADUS SAMADUL LADHI LAM YALID WALAM YULAD WALAM YAKUN LAHU KUFUWAN AHAD, AN TAGFIRA LI DHUNUBI INNAKA ANTAL GAFURUR RAHIM.

Ma'ana: Ya Allah lalle ni ina rokonka Ya Allah kai ne daya tilo, wanda ake nufinsa da bukatu, wanda bai Haifa ba kuma ba a haife shi ba, kuma babu daya da ya kasance tamka a gare shi, ka gafarta mun zunubaina lalle kai ne mai gafara mai rahama.

اللهم إني أسألك بأن لك الحمد لا إله إلا أنت وحدك لا شريك لك المنان يا بديع السموات والأرض يا ذا الجلال والإكرام، يا حي يا قيوم أسألك الجنة وأعوذ بك من النار

ALLAHUMMA INNI AS'ALUKA BI'ANNA LAKAL HAMDU LA'ILAHA ILLA ANTA WAHDAKA LA SHARIKA LAKA, ALMANNAN YA BADI'AS SAMAWATI WAL ARD, YADHAL JALALI WAL IKRAMI, YA HAYYU YA QAYYUM, AS'ALUKAL JANNATA WA A'UZU BIKA MINAN NAR.

Ma'ana: Ya Allah lalle ni ina rokonka saboda dukkan yabo da godiya takace, babu abin bauta bisa cancanta sai kai daya, ba ka da abokin tarayya, Ya mai kyauta kafin a roke shi, Ya wanda ya kagi halittan sammai da kasa, Ya ma'abocin girma da kyauta, Ya rayayye wanda yake tsaye a kan bayinSa, ina rokon ka aljanna kuma ina neman tsarinka daga wuta.

اللهم إنـي أعوذ بك من زوال نعمتك وتحول عافيتك وفجاءة نقمتك وجميع سخطك.

ALLAHUMMA INNI A'UDHU BIKA MIN ZAWALI NI'MATIKA, WA TAHAWWULI AFIYATIKA, WA FUJA'ATI NIQMATIKA, WA JAMI'I SAKHADIKA.

Ma'ana: Ya Allah lalle ni ina rokon ka da ka kare ni daga gushewar ni'imarka, da juyawar lafiyarka, da kuma fadowar ramuwar gayyayarka, da dukkan fushinka.

Idan kuma bakin ciki ne da damuwa suka sauka a kan ka, to sai ka fadi yadda Manzon Allah ya yi maka wasiyya:

لا إله إلا الله العظيم الحليم لا إلـه إلا الله رب العرش العظـيم لا إلـه إلا الله رب السموات ورب الأرض ورب العرش الكريم.

LA ILAHA ILLAL LAHUL AZIMUL HALIM, LA ILAHA ILLAL LAHU RABBUL ARSHIL AZIM, LA ILAHA ILLAL LAHU RABBUS SAMAWATI WA RABBUL ARDI WA RABBUL ARSHIL KARIM.

Ma'ana: Babu abin bauta bisa cancanta sai Allah mai girma mai hakuri, babu abin bauta bisa cancanta sai Allah Ubangijin al'arshi mai girma, babu abin bauta bisa cancanta, sai Allah Ubangijin sammai da kasa kuma Ubangijin al'arshi mai girma.

يا حي يا قيوم برحمتك أستغيث فألصح لي شأني ولا تكلني إلـي نفسـي طرفة عين.

YA HAYYU YA QAYYUM, BIRAHMATIKA ASTAGISU, FA'ASLIH LI SHA'NI KULAHU, WALA TAKILNI ILA NAFSI DARFATA 'AININ.

Ma'ana:Ya kai rayayye, kuma wanda ya ke tsaye a kan bayinsa ka temake ni saboda rahamarka,

ka gyara mun dukkan al'amurana, kuma kar ka bar ni da dibarata dai-dai da kiftawar ido.

لا إله إلا أنت سبحانك إني كنت من الظالمين

LA ILAHA ILLA ANTA SUBHANAKA INNI KUNTU MINAZ ZALIMINA.

Ma'ana: Babu abin bauta bisa cancanta sai kai, tsarki ya tabbabata a gare ka, lalle ni ina cikin wadanda suka zalunci kawunansu.

اللهم إني عبدك ابن عبدك ابن أمتك ناصيتي بيدك ماض في حكمك عدل في قضاؤك أسألك بكل اسم هو لك سيميت به نفسك أو أنزلته في كتابك أو علمته أحدا من خلقك أو استأثرت به في علم الغيب عندك أن تجعل القرءان ربيع قلبي ونور صدري وجلاء حزني وذهاب همي.

ALLAHUMMA INNI 'ABDUKA, IBNU 'ABDIKA, IBNU AMATIKA, NASIYATI BIYADIKA, MADIN FIYYA HUKMUKA, ADLUN FIYYA QADA'UKA, AS'LUKA BI KULLIS MIN HUWA LAKA, SAMMAITA BIHI NAFSAKA, AU ANZALTAHU FI KITABIKA, AU 'ALLAMTAHU AHADAN MIN KHALKIKA, AWIS TA'THARTA BIHI FI 'ILMIL GAIBI 'INDAKA, AN TAJ'ALAL QUR'ANA RABI'A

QALBI, WA NURA SADRI, WA JALA'A HUZNI, WA DHAHABA HAMMI.

Ma'ana: Ya Allah lalle ni bawanka ne, dan bawanka, kuma dan baiwarka, makwar-kwadata ta na hannunka ne, hukuncinka ya riga ya shude a kaina, kuma abin da kayi hukunci a kaina adalci ne, ina rokonka da duk wani suna naka, da ka sanya ma kanka, ko ka saukar da shi a cikin littafinka, ko ka sanar da shi wani daga cikin bayinka, ko kakebanta da saninshi a cikin ilimin gaibi dake wurinka, ka sanya alkur'ani ya zama bazarar zuciyata, kuma hasken kirjina, kuma mai kwaranye bakin cikina, kuma mai tafiyar da abin da ya dame ni.

اللهم إني أسألك العافيه في الدنيا والآخرة، اللهم إني أسلك العفو والعافية في ديني ودنياى وأهلى ومالى، اللهم استر عوراتى، وآمن روعاتى اللهم احفظنى من بين يدى ومن خلفى وعن يمينى وعن شمالى ومن فوقى وأعوذ بعظمتك أن أغتا ل من تحتى.

ALLAHUMMA INNI AS'ALUKAL 'AFIYATA FIDDUNYA WAL'AKHIRATI, ALLAHUMMA INNI AS'ALUKAL 'AFWA WAL'AFIYATA FI DINI WA

DUNYAYA WA AHLI WA MALI, ALLAHUMMAS TUR 'AURATI WA AMIN RAU'ATI ALLAHUMMAH FAZNI MIN BAINI YADAYYA WA MIN KHALFI WA AN YAMINI WA AN SHIMALI WA MIN FAUQI WA A'UDHU BI'AZAMATIKA AN UGTALA MIN TAHTI.

Ma'ana: Ya Allah lalle ni ina rokon ka samun lafiya a duniya da lahira, ya Allah lalle ni ina rokonka afuwa da samun lafiya a addinina da duniyata da iyalina da dukiyata.Ya Allah ka rufa mun asiri na, ka yi mun maganin abin da yake bani tsoro, Ya Allah ka kare ni ta gaba gareni, da ta bayana, da ta bangaren damana, da ta haguna, da kuma ta samana. kuma ina neman tsari da girmanka kada ayi mun kutungwila ta karkashina.

**SAKO NA HUDU**

Ya kai dan uwana mai girma! Na sani cewa dukkan mu mun shaida lalle Annabinmu, kuma Masoyinmu Annabi Muhammad (S.A.W) bawan Allah ne, kuma ManzonSa ne, kuma fiyayye a cikin halittun Allah, kuma amintaccen Allah a kan wahayinSa, Allah ya aiko shi domin ya zama rahama ga talikai, kuma ya sanya shi shugaba ga masu tsoron Allah, kuma shi ne hujjar Allah a kan bayinSa baki daya, ya isar da sakon Allah, kuma ya bayar da amanar dake wuyansa, kuma ya barmu a kan wata hanya daren ta tamkar rana ne (wurin haske), babu wanda zai karkace daga wannan hanya sai hallakakke, da shi Allah ya shiryar da mutane daga bata, kuma ya bude idanun mutane daga makanta, Allah ya daukaka ambatonsa, Allah ya buda zuciyarsa (domin daukan hakuri da fahimta) kuma ya sauke masa nauyinsa kuma Allah ya sanya kaskanci da wulakanci ga duk wanda ya saba umarninsa, tsira da amincin Ubangijina da albarkarSa su yawaita a

kansa, tare da mutanen gidansa da sahabbansa baki daya, da duk wanda yayi kira irin kiransa, kuma yabi sunnarsa, ya bibiyi gurabunsa, kuma ya bi kan hanyarsa, har zuwa ranar sakamako. Allah ya wajabta wa bayi su bi shi, kuma su so shi kuma su girmama shi, kuma suyi tsaye da hakkokinsa. To menene abin da ya wajaba a kan mu game da shi, Ya kai dan uwa mai girma?

Lalle akwai hakkoki masu girma a kanmu game da shi, daga ciki akwai:

1. Yawan yi mishi salati. Allah madaukakin Sarki yana cewa:

إن الله وملائكتـه يصـلون علـى النبـى يأيهـا الـذين آمنـوا صـلوا عليـه وسلموا تسليما (الأحزاب ٥٦)

Ma'ana: "Lalle Allah da Mala'ikunSa suna salati ga Annabi, ya ku wadanda da suka yi imani ku yi salati a gare shi, kuma ku yi sallama domin amintarwa a gare shi". (Ahzab 56)

Manzon Allah (s. a. w ) ya ce : "Duk wanda ya yi salati daya a gare ni, to Allah zai yi mishi salati sau goma".

Kuma ka sani ya kai dan'uwa, cewa mafificiyar siga wurin salati ga Manzon Allah (s. a. w) ita ce wadda ya karantar da sahabbansa ita kamar yadda ya tabbata a cikin Bukhari da Muslim yana cewa sahabbansa ku ce :

اللهم صلى على محمد وعلى آل محمد كما صليت على إبراهيم وعلى آل إبراهيم إنك حميد مجيد. وبارك على محمد وعلى آل محمد كما باركت على إبراهيم وعلى آل إبراهيم إنك حميد مجيد

ALLAHUMMA SALLI 'ALA MUHAMMADIN WA'ALA ALI MUHAMMAD, KAMA SALLAITA 'ALA IBRAHIM WA'ALA ALI IBRAHIM, INNAKA HAMIDUN MAJID WA BARIK 'ALA MUHAMMADIN WA'ALA ALI MUHAMMAD, KAMA BARAKTA 'ALA IBRAHIM WA 'ALA ALI IBRAHIM INNAKA HAMIDUN MAJID

Ma'ana: Ya Allah ka yi salati ga Muhammad, (s. a. w ) da mutanen gidansa, kamar yadda ka yi salati ga Ibrahim (a.s ) tare da mutanen gidansa,

lalle kai abin godewa ne, kuma abin girmamawa, Ya Allah ka yi albarka ga Muhammad (s. a. w) da mutanen gidansa kamar yadda ka yi albarka ga Ibrahim (a. s) tare da mutanen gidansa, lalle kai abin yabo ne, kuma abin girmamawa.

2. Son shi, so na gaskiya wanda yake a zuciya, da kuma gabatar da son shi a kan son kowa. Manzon Allah (s. a. w) ya ce: "Dayanku ba ya zama mai imani har sai na zama mafi soyuwa a gare shi fiye da 'ya'yansa da mahaifansa da dukkan sauran mutane". Daga cikin alamun son Manzon Allah (s. a. w) koyi da shi, da kuma yin ladabi da ladubbansa, da gabatar da umurninsa da sunnarsa a kan yardar kowa, da kuma barin duk abin da ya hana.

3. Yi masa biyayya cikin abin da ya yi umarni, da gaskata abin da ya ba da labari, da barin duk abin da ya yi hani a kansa, kuma ya tsawatar. Allah yana cewa.

وما آتاكم الرسول فخذوه وما نهاكم عنه فانتهوا (الحشر٧)

Ma'na: "Kuma duk abin da Manzon Allah ya ba ku to ku kama shi, kuma abin da ya hane ku to ku barshi". (Hashri 7)

kuma ya kara cewa:

قل إن كنتم تحبون الله فاتبعوني يحببكم الله ويغفر لكم ذنوبكم والله غفور الرحيم (ال عمران ٣١)

Ma'ana: "Kace: idan kun kasance kuna son Allah, to ku bi ni, Allah zai so ku, kuma ya gafarta muku zunubanku, kumaAllah mai gafara ne mai jin kai" (Ali Imrana 31)

Madaukakin Sarki ya kara cewa:

لقد كان لكم في رسول الله أسوة حسنة لمن كان يرجوا الله واليوم الآخر وذكر الله كثيرا (الاحزاب٢١ )

Ma'ana: "Lalle abin koyi mai kyau ya kasance gare ku, daga Manzon Allah, ga wanda ya kasance yana fatan rahamar Allah da ranar lahira. Kuma ya ambaci Allah da yawa." (Ahzab21)

4. Wajabcin kai hukunci zuwa ga sunnarsa da kuma yarda da hukuncinsa (s. a.w) da kuma barin

taurin kai da bijire wa abin da ya yi hukunci a kan shi. Allah yana cewa:

فلا وربك لا يؤمنون حتى يحكموك فيما شجر بينهم ثم لا يجدوا فى أنفسهم حرجا مما قضيت ويسلموا تسليما (النساء٦٥)

Ma'ana: "To a aha! Ina rantsuwa da Ubangijinka ba za su yi imani ba, sai sun yarda da hukuncinka ga abin da ya faru a tsakaninsu, sa'annan ba za su samu wani kunci a cikin zukatansu ba daga abin da ka hukunta, kuma su sallama sallamawa". (Nisa'i 65)

5. Kuma kar mu bauta wa Allah sai da abin da ya shar'anta mana, kuma ya yi mana umarni da shi, ba da ra'ayinmu, ko bida'a, ko da abin da zuciya take kauna, ko abin da muka samu iyaye da kakanni a kai, a a zamu yi bauta ne da abin da ya inganta daga gare shi (S.A.W) don shi ne dan sakon Ubangiji. Kuma hakika ya isar da sakon, kuma ya bayar da amanar da aka dora masa, kuma ya yi nasiha ga al'umma, babu wani alheri face ya nuna mana, kuma babu wani sharri face sai da ya gargade mu a kansa, Iyayenmu fansa

ne a gare shi. Hakika da aiko shi, Allah ya cika ni'imar sa a kan mu, kuma ya cika addini, babu wani alheri sai abin da ya shar'anta. Allah yana cewa:

اليوم أ كملت لكم دينكم وأتممت عليكم نعمتى ورضيت لكم الإسلام دينا (المائدة ٣)

Ma'ana: "A yau na kammala muku addininku, kuma na cika ni'imata a kanku, kuma na yarda da musulunci ya zama addini a gare ku. (Ma'ida 3)

## SAKO NA BIYAR

Dan uwana alhaji -Allah ya girmama ka da yin biyayya a gare shi- shin ka san abin da ya wajaba a kan al'umma su damu dashi a yau lokacin da masifu suka fada musu wannan na bin wannan? Gashi al'ummomin duniya sun fito fili suna kiyayya da su. Ya wajaba su damu da tsarkake da gyara akidarsu, don akida ta gari ita ce take bambanta su da wadanda ba su ba cikin al'ummomi, kuma ta hana su narkewa ko sajewa

da kafirai, kamar yadda ake so hakan ya faru, kuma ake iya bakin kokari wurin hakan, akida ta kwarai ita ce za ta hada kan al'umma, kuma su fuskatar da kiyayyarsu ga abokan gabansu kawai, wadanda suke fakon su. Akida ta kwarai ita ce za ta nuna ma al'umma kulle-kullen da abokan gaba suke musu da manufofinsu a kansu. Akida ita ce zata bambanta wannan al'ummar da duk sauran al'ummomi.

Yana daga cikin babukan akida masu mahimmanci - wanda shi ne zai kare wa al'umma, kasancewarsu (a bayan kasa) kuma ya hana su narkewa cikin kafirai, kuma ya ba su hadin kai – babin "ALWALA'U WAL BARA' " (So da Ki, wato son mutanen kwarai Musulmi, da kin kafirai). akidar"So da Ki" kafirai sun yi bakin kokarinsu wurin share ta cikin zukatan Musulmi da rayuwarsu ta yau da kullum, kuma sun yi amfani da kowace hanya don ganin hakan ya samu, to sai dai wane su! Ba za su iya share ta gaba daya ba, don Allah ya umurci kowane Musulmi ya nemi

tsari daga hanyar Yahudawa da Kirista sau goma sha bakwai a kullum alal akalla, Manzon Allah (s a.w) ya ce: "Babu sallah ga wanda bai karanta Fatiha ba".

Shin kuna ganin wannan akida za ta gushe a cikin zukatan Musulmi duk da kokarin haka da wasu suke yi har a cikin Musulmi? Alhali dare da rana suna karanta:

اهدنا الصراط المستقيم صراط الذين أنعمت عليهم غير المغضوب عليهم ولا الضالين (الفاتحة ٦-٧)

Ma'ana: "Ka shiryar da mu ga hanya madaidaiciya, hanyar wadanda ka yi wa ni'ima, ba wadanda ka yi fushi da su ba, kuma ba batattu ba". (Fatiha 6-7)

Wato ba hanyar wadanda ka yi fushi da su ba, su ne Yahudawa, ga dubun sani amma basu aiki da shi. Batattu kuma su ne kirista, wadanda suke bauta wa Allah a cikin jahilci da bata da dimuwa.

Lalle ayoyin littafin Allah da suke gaban kowane Musulmi suna hana Musulmi su karkata,

ko su ba da gaskiya ko su amince wa kowane kafiri, ballantana kulla kawance da shi, kuma kafircinsa ko wani irin launi ne, kuma ko daga wani irin jinsi ne ya fito.

Hakika Alkur'ani ya yi bayani a kan kadaita Allah wurin bauta, kuma ya yi bayanin soyayya da kiyayya ta dukkan bangarori, har sai da wannan al'umma ta zama ta bambanta da sauran al'ummomi, ta kasance tamkar jiki daya, a cikin ayyukanta da halayenta, hakika babu yarda a tsakanin Musulmin farko da kafirai, ballantana a gaskata labarinsu ko alkawuransu da zantuttukansu, kuma duk lokacin da akidar "ALWALA'U WAL BARA' " (So da Ki) tayi rauni a cikin zukatan mutane kuma suka jahilce ta, za ka ga sun karkata ga abokin gaba, shi kuma ya dandana musu mugunyar azaba, ya ci mutuncinsu.

Malamai sun yi bayani sun tsoratar a kan haka, daga cikin bayanansu:

**NA DAYA :** Lalle Musulmi yana karantawa cikin littafin Allah cewa: lalle kafiri tsakanin shi da Musulmi abu biyu ne: imma ya kasheshi mugun kisa, ko yayi kokarin mayar dashi cikin addininsa. Allah yana cewa:

إنهم إن يظهروا عليكم يرجموكم أويعيدوكم فى ملتهم ولن تفلحوا إذا أبدا (الكهف٢٠)

Ma'ana: "Lalle ne su idan sun sami dama a kanku to za su jefeku (kasheku da jifa ) ko kuma su mayar da ku cikin addininsu idan ha kan ya faru kuwa to, har abada ba zaku rabauta ba". (Kahfi 20)

**Nabiyu:** Musulmi mai hankali ya sani lalle kafirai za su ci gaba da ya kanmu, da cutar da mu, da makamai da makirce-makirce iri-iri, saboda su ba za su taba natsuwa ba, hankalin su ba zai kwanta ba har sai sun sanya mu mun yi ridda daga cikin addininmu madamar suna da iko. Allah yana cewa:

ولا يزالـون يقـاتلونكم حتــى يـردوكم عـن ديـنكم إن اسـتطاعوا ومـن يرتدد منكم عن دينـه فيمت وهو كـافر فأولئـك حبطـت أعمـالهم فـى الـدنيا والآخرة و أولئك أصحاب النار هم فيها خالدون (البقرة ٢١٧)

Ma'ana: "Kuma ba za su gushe ba suna yakan ku, har sai sun mayar da ku masu ridda daga barin addininku, idan sun samu damar ha kan, kuma duk wanda yayi ridda a cikinku daga barin addininsa har ya mutu yana kafiri, to wadannan 'yan wuta ne, su a cikinta dawwamammu ne." (Bakara 217)

**Na uku:** Yahudu da Kirista, duk yadda za ka yi kokarin yardar da su, da barin wani abu daga cikin addininka, ko wasu hakkokinka, ko ka yarda da kaskanci, kuma kana bin su cikin duk wani abu da suke so, to har abada ba za su yarda da kai ba, har sai ka bi hanyar su (ta kafirci), ka bar addininka da akidarka da 'yan'uwanka musulmi (sa'an nan sai ku zama daya da su) Allah yana cewa:

ولن ترضى عنك اليهود ولا النصارى حتى تتبع ملتهم (البقرة ١٢٠)

Ma'ana: "Kuma Yahudu da kirista ba za su yarda da kai ba, har sai ka bi irin akidarsu".( Bakara 120)

**Na hudu:** Kuma ko da sun nuna maka soyyaya da tausayi da son baiwa kowa hakkinsa, to duk wannan da baki ne bai kai zuciya ba, amma halayensu da kuma zukatansu, suna cike da kinmu (mu Musulmi) da kuma jin zafinmu. Allah yana cewa:

يرضونكم بأفواههم وتأبى قلوبهم وأكثرهم فاسقون (التوبة ٨)

Ma'ana: "Suna yardar da ku da bakunansu, amma zukatansu suna kin ha kan, kuma mafi yawan su fasikai ne". (Tauba 8)

**Na biyar:** Kuma su ba su gushewa suna manna mana kowace cuta. Idan wata musiba ta same mu, to abin nema ya samu, kuma abin farin cikin su ya sauka, kuma lalle duk mai bibiyar halayensu ha kan zai fito mishi fili, za ka iya ganewa ta hanyar abin da ke fitowa ta bakunansu, amma abin da zukatansu ke boyewa yafi girma. Allah yana cewa:

يأيها الذين آمنوا لا تتخذوا بطانة من دونكم لا يألونكم خبالا ودوا ما عنتم قد بدت البغضاء من أفواههم وما تخفي صدورهم أكبر قد بينا لكم الآيات إن كنتم تعقلون (آل عمران ١١٨)

Ma'ana: Ya ku wadanda suki imani kada ku riki abokan sirri daga waninku (abokan gaban ku) ba su takaita muku barna, kuma sun yi gurin abin da za ku cutu da shi, hakika kiyayya ta bayyana daga bakunansu, kuma abin da zukatansu ke boyowa ne mafi girma. Hakika mun bayyana muku ayoyi idan kun kasance masu hankalta. (Ali Imrana 118)

Kuma Allah ya kara cewa:

إن تمسسكم حسنة تسؤهم وإن تصبكم سيئة يفرحوا بها إن تصبروا وتتقوا لا يضركم كيدهم شيئا إن الله بما يعملون محيط (آل عمران ١٢٠)

Ma'ana: "Idan wani abin alheri ya shafe ku sai ya ba kanta musu rai, kuma idan wata cuta ta shafe ku sai suyi farin ciki da ita, kuma idan kunyi hakuri kuma ku kaji tsoron Allah kullin su ba ya cutar daku da komai, lalle ne Allah yana kewaye da abin da suke aikatawa. (Ali Imrana 120)

Kuma Allah ya ba da labari cewa idan sun kebe da junan su, suna wasu abubuwa da ke nuna tsananin fushi da bakin ciki a kan mu.(kamar cizon yatsa ) Allah ya ce:

وإذا خلوا عضوا عليكم الأنامل من الغيظ... (آل عمران ١١٩ )

Ma'ana: "Kuma idan sun kadaita sai su ciji yatsu a kanku don takaici". (Ali Imrana 119)

Abu ne sananne idan mutum ya yi fushi sai ka ga yana cizon yatsarsa, sai dai su wadannan yatsunsu duka sukan ciza, saboda tsananin jin zafinmu.

**Na shida:** Nuna so ga kafirai da uzurin tsoro a kan 'yan'uwa ko 'ya'ya (kada wani sharri ya same su), ba karbabben uzuri ba ne a wurin Allah, saboda Allah yana cewa:

يأيها الذين آمنوا لا تتخذوا عدوي وعدوكم أولياء تلقون إليهم بالمودة (الممتحنة ١)

Ma'ana: "Ya ku wadanda suka yi imani kada ku riki makiyana kuma makiyanku masoya, kuna jefa soyayya zuwa gare su". (Mumtahina 1)

Sa'an nan Allah ya ambaci shubuhar wadanda suke fakewa da dukiya da 'ya'ya sai ya ce:

لـن تـنفعكم أرحـامكم ولا أولادكـم يـوم القيامـة يفصـل بيـنكم والله بمـا تعملون بصير (الممتحنة ٣)

Ma'ana: "Zumuntarku ba zata amfane ku ba, haka kuma 'ya'yanku, a ranar kiyama (Allah) zai rarrabe tsakaninku, kuma Allah mai gani ne ga abin da kuke aikatawa". (Mumtahina 3)

**Na bakwai:** Lalle kafirai ko da sun saba a tsakninsu, kuma suna yakin junansu, to kansu a hade yake, idan abokin gabansu shi ne Musulmi, to suna zama al'umma daya masu son junansu, kuma lalle Musulmi idan basu hada kansu ba, kama sun so junansu, hakika barna za ta fada musu, da fitina mai girma. Kamar yadda Allah ya ce:

والـذين كفروا بعضـهم أوليـاء بعض إلا تفعلـوه تكـن فتنـة فـي الأرض وفساد كبير (الأنفال٧٣)

Ma'ana: "Kuma wadanda suka kafirta, sashensu masoya sashe ne, idan baku aikata haka ba (ku

Musulmi) to wata fitina zata kasance a bayan kasa da fasadi babba". (Anfal 73)

**Na takwas:** Huzaifah (R.A) yana cewa: "Dayanku ba ya jin tsoro ya zama Bayahude ko ya zama Kirista, alhali shi bai sani ba, saboda wannan ayar:

يأيها الذين آمنوا لا تتخذوا اليهود والنصارى أولياء بعضهم أولياء بعض ومن يتولهم منكم فإنه منهم إن الله لا يهدي القوم الظالمين (المائدة ٥١)

Ma'ana: "Ya ku wadanda suka yi imani, kada ku riki Yahudu da Kirista masoya, sashensu masoya sashe ne, kuma duk wanda ya nuna musu soyayya yana daga cikin su. Lalle Allah baya shiryar da mutane azzalumai". (Ma'ida 51)

Kuma Allah ya hana son iyaye da 'yan'uwa idan sun kasance kafirai, to ina ga waninsu? Allah yana cewa:

يأيها الذين آمنوا تتخذوا آباءكم وإخوانكم أولياء إن استحبوا الكفر علي الإيمان ومن يتولهم منكم فأولئك هم الظالمون (التوبة ٢٣)

Ma'ana: "Ya ku wadanda suka yi imani kada ku riki Ubaninku da 'yan'uwanku masoya idan sun nuna son kafirci a kan imani, kuma duk wanda ya nuna musu so a cikin ku, to wadannan su ne azzalumai". (Tauba 23)

Kuma Allah ya hana a so kafiri ko da ya kasance uba ko da ko dan'uwa, kamar yadda ya ke fadi:

لا تجد قوما يؤمنون بالله واليوم الآخر يوادون من حاد الله ورسوله ولو كانوا آباءهم أو أبناءهم أو إخوانهم أو عشرتهم أولئك كتب فى قلوبهم الإيمان وأيدهم بروح منه ... (المجادلة ٢٢)

Ma'ana: "Baza ka sami mutane sunyi imani da Allah da ranar lahira, suna nuna soyayya ga wanda ya saba wa Allah da Manzonshi ko da sun kasance iyayensu ne, ko 'ya'yansu ko 'yan'uwansu ko danginsu, wadannan su ne Allah ya rubuta imani a cikin zukatansu kuma ya karfafasu da wani ruhi da ga wurinsa". (Mujadala 22)

Kuma ka sani, Ya kai dan uwa mai girma, lalle daga cikin abubuwan da suke nuna son kafirai

(wanda aka hana mu) abin da malamai suka fadi kamar:

1. kwaikwayon su a wurin halaye da kayan sawa da sauransu Manzon Allah (S.A.W) yana cewa:

"Duk wanda ya kwaikwayi wasu mutane, to ya zama daya daga cikinsu"

2. Goyon bayansu, ko taimakonsu a kan Musulmi, wannan yana cikin abubuwan da ke warware musuluncin mutum, kuma sababi ne daga cikin sabubban ridda.

3. Ba su manyan mukamai, wadanda da wadannan mukaman ne suke leken asiran Musulmi, haka kuma mayar dasu abokan asiri, ko 'yan shawara.

4. Taya su farin ciki a lokacin bukukuwan idinsu, ko taimakonsu a kan hakan, ko taya su murna.

## SAKO NA SHIDA

Dan uwana Alhaji – Allah ya kare ka daga kowane mugun abu- ga bayani a kan rukunin musulunci mafi girma bayan shahada, wato salla. Salla ita ce wasiyyar Manzon Allah (S.A.W) ta karshe lokacin da zai rasu , lokacin da yake cewa: "(Ina horon ku da tsai da) salla, (ina horon ku da tsai da) salla.

Hakika wasu Musulmi suna yin wasa da ita, ko saboda sun jahilci hukunce-hukuncenta, ko kuma saboda sakaci da halin ko-in-kula, wasu daga cikinsu suna jinkirta ta har lokacinta ya fita, wasu kuma basu yin ta cikin jam'i, ba tare da wani uzuri ba, wasu basu ma damu da ita ba! Masu hakan suna cikin hadari mai girma, saboda salla ita ce ginshikin addinin musulunci ita ce take rabewa tsakanin Musulmi da kafiri, kuma hakika malamai sun yi bayani cewa duk wanda ya bar salla to ya kafirta! Kamar yadda Allah yake cewa:

فإن تابوا وأقاموا الصلاة وآتوا الزكاة فإخوانكم في الدين...(التوبة ١١)

Ma'ana:"Sa'an nan idan sun tuba, kuma suka tsayar da salla, kuma suka bayar da zakka, to (sun zama) 'yan'uwanku a cikin addini". (Tauba 11)

Wannan aya ta yi nuni cewa duk wanda ya bar salla to ba dan'uwanmu ba ne. Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: "Lalle tsakanin mutum (Musulmi) da (ya zama) mushriki ko kafiri, shi ne barin salla".

An karbo Hadisi daga Buraida (R.A) ya ce: "Na ji Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: "Abin da ke tsakaninmu da su, shi ne salla, duk wanda ya bar ta to ya kafirta".

Abdullahi bin shakik ya ce: "Sahabban Manzon Allah (S.A.W) ba su ganin barin wani aiki kafirci ne, sai dai salla".

Dan'uwana Alhaji, lalle barin salla –bayan hujja ta tsayu- yana tattare da wasu abubuwa masu hadari, kamar haka:

1. Duk wanda ya bar salla, to waliccinsa a kan 'yayansa da matansa ya saraya.

2. 'Yan'uwanshi ba za su gaje shi ba, shi ma ba zai gaje su ba.

3. Shiga Makka ya haramta a gare shi, saboda fadin Allah:

يأيها الذين آمنوا إنما الشركون نجس فلا يقربوا المسجد الحرام بعد عامهم هذا ... (التوبة ٢٨)

Ma'ana: "Ya ku wadanda suka yi imani, lalle mushrikai najasa ne, saboda haka kada su kusanci masallaci mai alfarma, a bayan shekararsu wannan." (Tauba 28)

4. Baya halatta a ci yankansa.

5. Idan ya mutu ba za a yi mi shi salla ba, ba za a nema masa gafara ba.

6. Idan matarsa musulma ce, kuma tana salla to, za a raba tsakaninsu.

7. Ba za a rufe shi a makabartar Musulmi ba.

Kuma ka sani, Ya kai dan'uwa Alhaji – Allah ya kiyaye ka, kuma ya kare ka – lalle wajibi ne a kanka ka yi salla a kan lokacinta kuma cikin jam'i, ba ya halatta ka yi salla a gidanka, sai idan kana da uzuri, kamar tsoro ko rashin lafiya, Allah yana cewa:

واركعوا مع الراكعين (البقرة ٤٣)

Ma'ana: "Kuma ku yi ruku'i tare da masu ruku'i." (Bakara 43)

Hakika Allah ya wajabta salla cikin jam'i hatta lokacin yaki, da fuskantar abokan gaba. Da zai yiwu a yi wa wani uzuri, ya bar sallar jam'i, to da mayaka sun fi kowa cancanta da a yi musu uzuri, su yi salla daban-daban. Amma ina! Allah ya wajabta musu sallar jam'i kamar yadda yake cewa:

وإذا كنت فيهم فأقمت لهم الصلاة فلتقم طائفة منهم معك وليأخذوا أسلحتهم فإذا سجدوا فليكونوا من ورائكم ولتأت طائفة أخرى لم يصلوا فليصلو معك وليأخذوا حذرهم وأسلحتهم (النساء١٠٢)

Ma'ana: "Kuma idan ka kasance a cikinsu (lokacin yaki) sai ka tsayar musu da salla, to wata kungiya daga gare su, ta tsaya tare da kai, kuma sai su rike makaminsu, sa'an nan idan sun yi salla to sai su kasance daga bayanku, kuma wata kungiya ta daban ta wadanda ba su yi salla ba, sai ta zo sa'an nan su yi salla tare da kai, kuma su rike shirinsu da makamansu. (Nisa'i 102)

Bukhari da muslim sun ruwaito daga Abu Hurairah (R.A) ya ce: "Manzon Alllah (S.A.W) ya ce: " Hakika na yi niyya a tsayar da salla, sa'an nan in umurci wani mutum ya yi wa mutane salla, sa'an nan in tafi tare da wasu mutane tare da su akwai bakunan wuta, zuwa wurin wasu mutane da ba su zuwa salla (a cikin jam'i) in kona musu gidajensu."

Kuma Muslim ya ruwaito daga Abdullahi bin Mas'ud (R.A) ya ce: "Hakika na gan mu, (a cikinmu) ba mai kin zuwa sallah (a masallaci) sai munafiki wanda munafuncinsa ya bayyana, ko mara lafiya, duk da cewa mara lafiyan ma (za ka

gan shi) tsakanin mutane biyu (yana gorare da su) har sai ya zo salla (a masallaci).

(Muslim) Ya kara ruwaito wa daga Ibnu Mas'ud ya ce: "Duk wanda yake so ya hadu da Allah gobe kiyama yana Musulmi, to ya kiyaye wadannan salloli a inda ake kiran su (masallaci ) lalle Allah ya shar'anta wa Annabinku sunnonin shiriya, kuma lalle salla tana cikin sunnonin shiriya, da za ku yi salla a gidajenku, kamar yadda wannan mai zama a gidansa yake yi, da kun bar sunnar Annabinku, kuma idan kuka bar sunnar Annabinku, to da kun bace. Babu wani mutum da zai yi alwalla kuma ya kyautata alwallar, sa'an nan ya tafi wani masallaci daga cikin wadannan masallatan face sai Allah ya rubuta masa lada ga kowane taku da ya yi, kuma ya daga darajarsa da shi, kuma ya yafe mishi laifi guda daya (da kowane taku ) hakika na gan mu, babu mai kin zuwa salla sai munafiki wanda munafuncinsa ya fito fili, kuma hakika za ka ga an

taho da mutum (mara lafiya ) a tsakanin mutum biyu har sai an tsayar dashi a cikin sahu."

Kuma a cikin Sahihu Muslim daga Abu Huraira (R.A): "Wani mutum makaho ya zo ya ce: Ya Manzon Allah (S.A.W), lalle ni bani da dan jagora da zai rinka kawo ni masallaci, shin ina da wani uzuri in yi salla a gida? Sai Manzon Allah (S.A.W) ya ce: Shin kana jin kiran salla? Ya ce kwarai ina ji, sai ya ce: To ka amsa (ni ba ni da uzurin da zan iya yi maka )"

Ka dubi wannan Hadisi, Ya kai dan uwa. Duk da cewa Manzon Allah (S.A.W) mai tausayi ne mai jin kai amma ya ki yi ma wannan makahon uzuri ( yayi salla a gida ) wannan ya ishe ka dalili a kan wajabcin sallar jam'i.

Kuma ya wajaba a gare ka ka kula da wannan al'amari, kuma ka yi gaggawa zuwa gare shi, kuma ka yi wa 'ya'yanka da mutanen gidanka da makwabtanka da sauran 'yan'uwanka Musulmi wasiyya a kan sallar jam'i, da haka ne za ka kasance ka bi umurnin Allah da ManzonSa

(S.A.W) kuma ka guji kama da munafukai. Allah yayi mana muwafaka ga abin da yake so, kuma ya yarda da shi, kuma ya kare mu gaba daya daga sharrin kawunanmu da miyagun ayyukanmu, lalle Allah Mai kyauta ne Mai girma.

### SAKO NA BAKWAI

Dan uwana Musulmi, saboda raunin imani da karancinsa, da ya yi yawa a cikin Musulmi, an samu wanda yake dagula musu rayuwansu, ya kuma bata musu addinsu da duniyarsu, da wasu miyagun abubuwa, lokacin da Musulmi suke da karfi, sun yaki wadannan abubuwan, kuma suka kashe ma'abotansu. Daga cikin wadannan miyagun abubuwa, akawai bokanci da bokaye. Dan'uwana Musulmi -Allah ya kare ka daga kowane mugun abu- bokanci yana cikin kaba'irai! Kuma Manzon Allah ya hada shi da shirka ya ce: "Ku nisanci abubuwa bakwai masu hallakarwa: shirka da Allah, da kuma bokanci…" Manzon Allah (S.A.W) ya barranta daga kowane boka,

kuma ya bada labari cewa, bashi cikin wannan al'umma. (wato ba Musulmi ba ne)

An karbo daga Imran bni Husain (R.A) ya ce: "Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Ba shi tare da mu, duk wanda ya yi camfi ko a ka yi mishi canfi (da yardansa) ko ya yi duba ko ya sa a ka yi mishi duba, ko ya yi bokanci ko ya sa a ka yi mishi bokanci."

Kuma lalle gaskata shi yana kai mutum zuwa ga kafirci, Allah ya kare mu daga gare shi. Ibnu Mas'ud (R.A) ya ce: "Duk wanda ya je wurin dan duba ko boka ko mai tsafi, kuma ya gaskata shi a kan abin da ya ke fadi, hakika ya kafirta da abin da a ka aiko Annabi Muhammad (S.A.W) da shi".

Kuma ukubar wanda yake bokanci shi ne a sare shi da takobi, kamar yadda Imam Ahmad ya ruwaito daga Bujalah ya ce: "Umar binil Khaddab ya rubuta (ya aika wa hakimansa) cewa: "Ku kashe duk wani boka namiji ko mace. ya ce : sai muka kashe bokaye uku."

An karbo daga Jundub (R.A) ya ce: "Haddin boka shi ne: a sare kansa da takobi".

Ka sani ya kai dan'uwa, lalle a hada neman magani da sabon Allah, kamar zuwa wurin bokaye da matsafa, da 'yan duba, Allah ne kadai mai ba da lafiya, kuma bai sa warakar wani a cikin wannan al'umma cikin abin da ya haramta musu ba, kamar yadda Manzon Allah (S.A.W) ya bada labari.

Kuma a kan yi maganin sihiri ne da wadannan abubuwa (Allah ya tsare mu ):

1. Kona abin da aka yi sihirin dashi idan an gan shi kamar yadda Manzon Allah (S.A.W) ya yi.

2. Daga cikin magunguna masu amfani akwai yin magani da maganar Allah (Alkur'ani) da kuma adduo'in Manzon Allah (S.A.W) daga ciki akwai karanta "Falaki da Nasi"

3. Daga cikin rukyar da ta zo daga Manzon Allah (S.A.W) lokacin da yake wa Hassan Husain addu'a:

أعيذكما بكلمات الله التامة من كل شيطان وهامة ومن كل عين لامة

U'IDHUKUMA BIKALIMATIL LAHIT TAMAH, MIN KULLI SHAIDANIN WA HAMMAH WAMIN KULLI AININ LAMMAH.

Ma'ana: Ina nema muku tsari wurin Allah da kalmominSa cikakku, daga sharrin shaidan, da kowane abu mai cutarwa, kuma da duk wani mai kambun baka (ko kanbin ido)".

Da fadinsa:

بسم الله أرقيك والله يشفيك من كل داء يؤذيك

BISMILLAHI ARQIKA WALLAHU YASHFIKA MIN KULLI DA'IN YU'UDHIKA.

Ma'ana: Ina maka tofi da sunan Allah, Allah ya warkar da kai daga kowane ciwo da yake cutar da kai.

Da fadinsa.

أسأل الله العظيم رب العرش الكريم أن يشفيك (سبع مرات )

AS'ALULLAHAL AZIM RABAL 'ARSHIL KARIM AN YASHFIYAKA (sau bakwai)

Ma'ana: Ina rokon Allah Mai girma Ubangijin al'arshi mai girma, da ya baka lafiya.

Da fadinsa:

أذهب البأس رب الناس واشف أنت الشافى لا شفاء إلا شفاؤك شفاء لا يغادر سقما

ADHHIBIL BA'S RABBAN NAS, WASHFI ANTASH SHAFI LA SHIFA'A ILLA SHIFA'UKA, SHIFA'AN LA YUGADIRU SAQAMAN.

Ma'ana: Ka tafiyar da cutar, ya Ubangijin mutane, kuma ka warkar, kai ne mai warkarwa, babu waraka sai warakarka, waraka wadda ba ta barin cuta.

daga cikin abubuwa da ke kare mutum daga kowace cuta, da izinin Allah akwai: Nace wa zikirin safiya da maraice, daga ayoyin Alkur'ani da abin da ya inganta daga sunnar Manzon Allah (S.A.W)

4. Daga cikin manyan abubuwa na neman kariya daga sharrin masu sihiri akwai: Dawwama akan da'ar Allah da bautanSa. Saboda da yawa

cikin mutane suna sakaci, sai ka ga suna aikata abin da Allah ya hana, sai wani ciwo ya kama su! to a nan za su tuna da Ubangijinsu, alhali Manzon Allah (S.A.W) ya ce lokacin da yake wa Ibnu Abbas wasiyya: "Ka tuna da Allah kana cikin wadata, sai ya tuna da kai idan ka shiga cikin kunci". Duk wanda ya tuna da Allah lokacin da yake da lafiya da karfi, sai Allah ya tuna da shi lokacin da yayi rauni ya kamu da rashin lafiya.

**SAKO NA TAKWAS**

Shin ka sani ya kai dan'uwa -Allah ya kare ka- cewa hali mai kyau yana daga cikin manyan ayyukan da suka fi soyuwa ga Allah da ManzonSa. Ya tabbata a Hadisin da aka karbo daga Sa'ad bni Abi Wakkas (R.A), lalle Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Lalle Allah yana son halayen girma, kuma ba ya son halayen karanta".

Shin ka san me ake cema hali na gari? Abdullahi bin Mubarak ya yi mana bayanin me ake ce ma hali na gari ya ce: "Shi ne sakin fuska,

da yi wa mutane alheri (wato kyauta ) da kuma kamewa daga cutarwa".

Dan'uwana mai girma, Lalle muna wani lokacin da halaye suka lalace, halaye na gari, wadanda a ka rasa su hatta wurin wasu manyan mutane, sai halayen suka zama kamar ba wasu abubuwa ba ne masu mahimmanci.

Lalle halaye na gari suna da wani matsayi mai girma a Musulunci. Ba ka ji Manzon Allah (S.A.W) ya cewa ba: "Lalle an aiko ni ne domin in cika halaye na gari." A wata riwaya ya ce: "Lalle ni ba a aiko ni ba, face don in cika manyan halaye."

Kamar ya takaita abin da aka aiko shi da shi a kan wannan al'amari.

Hakika akwai wasu manyan al'amura tattare da halaye na gari. daga ciki akwai:

1. An takaita da'a ga Allah a kyawun hali. An karbo Hadisi daga Nawwas bni sam'an (R.A) ya ce: "Na tambayi Manzon Allah (S.A.W) a kan da'a ga Allah da kuma zunubi, sai ya ce: da'a ga Allah

ita ce kyawun hali, shi kuma zunubi, shi ne abin da ke sosa maka rai, kuma baka so kowa ya ganka kana yi."

2. Kyawun hali ya na cikin ayyuka da suke saurin shigar da mutun aljanna. kamar yadda ya zo a Hadisin Abu Huraira (R.A) ya ce: "An tambayi Manzon Allah (S.A.W) game da abin da yake yawan shigar da mutane aljanna, sai ya ce: "Jin tsoron Allah, da kuma kyawun hali."Kuma a ka tambaye shi a kan abin da yake yawan shigar da mutane wuta, sai ya ce: "Baki da farji". (wato yawan surutu, da zuwa ma abin da Allah ya haramta na daga jima'i)

3. Hali na gari yana nauyaya mizanin mutum ranar kiyama. An karbo Hadisi daga Abud Darda'i (R.A) cewa: Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Babu wani abu a mizanin mumini wanda ya fi kyawun hali nauyi, kuma lalle Allah yana kin mai alfasha, mai batsa".

4. Duk wanda ya yi kwalliya da halaye masu kyau to Manzon Allah (S.A.W) ya yi mishi lamunin

cewa yana da gida a aljanna ta sama. An karbo Hadisi daga Abu Umama (R.A), ya ce: Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Nayi alkawarin gida a gefen aljanna ga wanda ya bar gardama ko da yana da gaskiya, da kuma gida a tsakiyar aljanna ga wanda ya bar karya ko da ba a yake yi, da kuma gida a aljanna ta sama ga wanda halayensa suka kyautata".

5. Lalle mai halaye na gari zai samu darajar mai azumi mai tsayuwan dare. An karbo Hadisi daga A'isha (R.A) ta ce: "Na ji Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: "Lalle mumini yana kaiwa da kyawun halayensa darajar mai azumi kuma mai tsayuwar dare".

6. Masu halaye na gari, su ne na gaba-gaba, a majalisar Manzon Allah (S.A.W) ranar kiyama. An karbo Hadisi daga Jabir (R.A) cewa: "lalle Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Lalle wadanda na fi so a cikinku, kuma suka fi kusa da ni a majalisata ranar kiyama, su ne masu kyawun hali. Kuma wadanda na fi ki a cikinku, kuma suke nesa da ni

a majalisata ranar kiyama, su ne masu yawan surutu kuma masu karkata baki (idan suna magana saboda girman kai) kuma masu nuna wa mutane sun sani (saboda yawan surutunsu). sai suka ce ya Manzon Allah: "lalle mun san masu yawan surutu, to su waye masu karkata baki, kuma masu nuna sun sani? Sai ya ce: su ne masu girman kai."

7. Lalle hali mai kyau, shi ne halin manyan mutane mafifita. Ya zo a cikin Hadisin Bukhari da Muslim daga Abdullhi bni Amr: "Lalle Manzon Allah ya kasance yana cewa: lalle zababbu a cikinku, su ne wadanda suka fi kowa hali mai kyau".

Ya dan'uwana mai girma! Shin za a iya samun Musulmin da zai ki hali mai kyau bayan ya san girmansa da falalarsa? a a ( ina tunanin ba za a samu ba ).

Ya za a yi Musulmi ya ki hali na gari, alhali shi ma yana son madaukakin matsayi a majalisar Manzon Allah (S.A.W), kuma yana kwadayin

halaye irin na Annabta? Ya zo cikin Hadisin da Bukhari da Muslim suka ruwaito daga Anas (R.A) ya ce: "Manzon Allah (S.A.W) ya kasance ya fi kowa hali na gari." Ya Kuma zo a Hadisin Bukhari da Muslim daga Abdullahi bni Amr ya ce: "Manzon Allah bai kasance mai alfasha ba, kuma ba mai son alfasha ba ne."

Dan'uwana mai girma, lalle hali na gari duk da falalarsa da ka sani, to amma fa'idar da yake tattare da ita, tana komawa zuwa gare ka ne, abin da ka shuka shi ne za ka girba, hali mai kyau hali ne na rahama, kuma da shi ne za ka sami rahamar Allah wanda ya fi kowa rahama. Ya zo a Hadisi ingantacce cewa Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Ka ji tausayin wanda ke kasa, sai Wanda ya ke sama (wato Allah) ya tausaya maka".

Dabarini ya ruwaito Hadisi da Isnadi Hasan (dangane mai kyau) cewa: "wadanda Allah ke tausaya wa kawai cikin bayinSa sune masu tausayi"

Kuma an karbo Hadisi daga Abdullahi bin Amr: " Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Masu tausayi, Allah Madaukakin Sarki yana tausaya musu, ku tausaya wa wadanda su ke kasa, sai Wanda ya ke sama ya tausaya muku."

Abin da ka shuka shi ne za ka girba, duk wanda ba ya tausaya wa mutane to shi ma baza a tausaya masa ba.

Bukhari da Muslim sun ruwaito daga Jarir bin Abdullahi cewa: " Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Duk wanda ba ya tausaya wa mutane, to shi ma Allah ba zai tausaya mishi ba."

Idan kana son Allah ya ji kanka, to kai ma ka ji kan kanka, kuma ka ji kan mutane, kar ka zalunci waninka, ka tausaya wa jahili da Ilminka, ka tausaya wa kaskantacce da girmanka, ka tausaya wa talaka da dukiyarka, ka tausayawa babba da karami da tausasawarka, ka tausaya wa masu sabo da wa'azinka, ka tausaya wa dabbobi da tausasawarka da dauke fushinka a kansu, a

takaice rahamar Allah tana kusa da wanda ya ke tausayin bayinSa.

Don Allah kalli hali na nasiha da temakon Musulmi, ya zo a Hadisin da Bukhari da Muslim suka ruwaito: "Lalle Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Duk wanda ya biya wa dan'uwansa bukatarsa, to shi ma Allah zai biya masa bukatarsa". Kwarai kuwa, abin da ka shuka ai shi ne za ka girba, idan ka temaki dan'uwanka a kan bukatarsa ka biya masa ita, sai Allah Madukakin Sarki ya temake ka a kan taka bukatar, kuma ya biya maka ita. Sa'an nan ya ce: "Duk wanda ya suturta dan'uwansa a nan duniya, to sai Allah ya suturta shi a lahira".

A Hadisin Muslim kuwa sai ya ce: "Duk wanda ya kwaranye wa wani Musulmi wani bakin ciki daga cikin bakin cikin duniya, to Allah zai kwaranye masa wani bakin ciki daga cikin bakin cikin lahira, duk wanda ya temaki wanda ya shiga wani mawuyacin hali a duniya, to Allah zai temake shi a nan duniya, da gobe kiyama (ranar da kowa zai shiga cikin mawuyacin hali). Kuma

duk wanda ya suturta Musulmi, to Allah zai suturta shi a gobe kiyama. Kuma Allah ba zai gushe ba yana temakon bawa madamar wannan bawan yana temakon dan'uwansa (Musulmi)".

Ya dan'uwana lalle duk wanda yake kallon halin wasu Alhazan a yau to zai ga abin mamaki! Zai ga karya a maimakon gaskiya, zai ga tsanani a maimakon tausayi, zai ga cin amana a maimakon cika alkawari, zai ga fushi a maimakon hakuri da yafe wa mutane, zai ga cutarwa a maimakon kyautatawa, zai ga rowa a maimakon kyauta, zai ga babakere a wurin zama da abinci ko abin sha, a maimakon fifita wasu a kan kawunansu, zai ga girman kai a maimakon tawalu'u zai ga zalunci a maimakon adalci.

Sai ka ga mutum yana tambaya a cikin zuciyarsa: shin wannan Musulmi ne kuwa? (idan Musulmi ne) to ina kamun kai? Ina amana? Ina kunya? Ina tausayin makaskanci? Ina tausayi ga miskini? Ina son juna? Ina tausayin muminai?

Dan'uwana hakika za ka ga masu irin wadannan halaye marasa kyau, za ka ga wanda zai ture ka a wurare masu tsarki, ko wanda zai cutar da kai a wurin Dawafi ko Sa'ayi, da wanda zai cutar da kai da wari mara dadi, kamar warin taba da sauransu, kuma za ka ga ha kan bai dame shi ba, hakika za ka ga wanda zai gaya maka maganganu marasa dadi, da wanda bai damu da girmama da tsarkake wuraren nan masu tsarki ba, fuskacin jefa datti da kazamce-kazamce, ko kuma warin sabon Allah da ayyukan bidi'a, da kuma barna ko cutar da mutane.

To ya za ka yi da irin wadannan mutane? Shin za ka rama mummuna da mummuna ne? idan muka yi haka to ba mu da bambanci da su, kuma mu ma mun temaka wurin yada mugun hali a kasa mai tsarki, da wurare masu alfarma. Abin da ya zama wajibi a kaina, ni da kai, game da irin wadannan mutane, shi ne hakuri da yafiya, da kuma tunkude cuta da abin da shi ne mafi kyau, Allah yana cewa:

والكـاظمين الغـيظ والعـافين عـن النـاس والله يحـب المحسـنين (آل عمران ١٣٤)

Ma'ana: "Kuma suke masu hadiyewar fushi, kuma masu yafe wa mutane laifi. Kuma Allah yana son masu kyautatawa." (Ali Imrana 134)

Kuma ya sake fadi yana wasafta muminai:

ويدرؤون بالحسنة السيئة أولئك لهم عقبى الدار (الرعد ٢٢)

Ma'ana: "Kuma suna tunkude mummunan aiki da mai kyau. Wadancan suna da akibar gida mai kyau." (Ra'ad 22)

Kuma Allah ya sake cewa:

ولا تستوي الحسنة ولا السيئة ادفع بالتي هي أحسن فإذا الذي بينك وبينه عداوة كأنه ولي حميم (فصلت ٣٤)

Ma'ana: "Kuma kyautatawa ba ta dai-daita, kuma haka munanawa. Ka tunkude cuta da abin da yake mafi kyau, sai ga shi wanda akwai kiyayya a tsakaninka da tsakaninsa, kamar dai shi majibinci ne, masoyi". (Fussilat 34)

Muslim ya ruwaito daga Abu Huraira (R.A): "Llalle Manzon (S.A.W) ya ce: "Sadaka ba ta taba

rage wata dukiya ba, kuma Allah ba ya kara wa bawa idan ya yi afuwa sai dai daukaka, kuma bawa bai taba tawalu'u saboda Allah ba, face sai Allah ya daukaka shi."

Shin ba za mu yi koyi da Manzon Allah (S.A.W) ba? Shin ba shi ne fiyayyen halitta ba, kuma wanda ya fi su falala, da kyauta? Duk da haka bai taba yin ramuwar gayya domin kansa ba. A'isha (R.A) ta ce: "Manzon Allah (S.A.W) bai taba ramuwar gayya saboda kansa ba, sai dai idan an saba wa Allah to sai ya yi ramuwar gayya saboda Allah". Bukhari da Muslim suka ruwaito.

A cikin Muslim daga A'isha (R.A): "Ba a taba yi wa Manzon Allah (S.A.W) wani abu ba ya rama." An karbo Hadisi daga Anas bni Malik ya ce: "Na kasance ina tafiya tare da Manzon Allah (S.A.W) ya sanya wata riga wadda aka yi ta a Najran, gefenta mai kauri ne, sai wani mutumin kauye ya same shi a kan hanya, sai ya fizgo shi fizga mai tsanani! Na kalli wuyar Manzon Allah (S.A.W) sai ga shi ta karce wuyarsa saboda tsananin fizgar

da ya yi masa! Sa'an nan ya ce masa: Ya Muhammad, ka sa a bani dukiyar Allah wadda take wurinka, sai ya waigo ya kalle shi, sa'an nan ya yi murmushi, kuma ya sa a ka bashi dukiya mai yawa".

To mu me yasa muke fushi saboda abu kadan da wani musulmi ya yi mana, kuma muke fushi saboda wani dan kuskure da dan'uwanmu zai mana, ka ga muna ciccikowar fushi muna tutture juna kai kace mun fito yaki ne da abokin gaba? Shin ba Allah yana cewa ba:

إنما المؤمون إخوة (الحجرات ١٠)

Ma'ana: "Hakika Muminai 'yan uwan juna kawai ne." (Hujurat 10)

Shin ba Annabinmu kuma masoyinmu Manzon Allah (S.A.W) ya fadi ba: "Misalin muminai wurin soyayya da junan su, da kuma tausayin junansu, da jin kan junansu, kamar jiki daya ne, idan wata gaba ta kamu da ciwo, sai sauran jiki ya kamu da zazzabi da rashin barci". Idan ba mu sawa kawunanmu hakuri da cije rai a wadannan wurare

masu tsarki ba to yaushe ne za mu sawa kawunanmu hakurin?

Ya kamata mu koma zuwa kawunanmu mu yi kokari wurin aikin alheri da kyautatawa, kuma mu yi wa kawunanmu hisabi, ko Allah ya shiryar da mu hanyarsa madaidaiciya. Allah yana cewa:

والذين جاهدوا فينا لنهدينهم سبلنا وإن الله لمع المحسنين (العنكبوت ٦٩)

Ma'ana: "Kuma wadannan da suka yi kokari ga neman yardarmu, lalle zamu shiryar da su ga hanyoyinmu, kuma lalle Allah, tabbas yana tare da masu kyautatawa". (Ankabut 69)

Allah yasa ka dace da abin da ya ke so kuma ya yarda da shi. Kuma ya sanya ka mai albarka duk inda kake, kuma ya mayar da kai zuwa ga iyalanka, da garinka lafiya lau. Amin.

## SAKO NA TARA

Ya yan'uwana Alhazai masu girma, bai zama boyayye a gare ku ba, cewa: Lalle cakudar mata da maza, a wuraren aiki, da kasuwanni da wuraren hutawa, da bukukuwa, yana daga cikin sabubban rushewar al'umma, da kuma bacin halaye, da rabuwar iyali, da yaduwar laifuffuka, da lalacewar harkar tsaro.

Wannan shi ne cakuduwar da kasashen kafirci ma suna kuka da shi, kullum suna fatar rabuwa da shi, saboda abin da ya ja musu na bala'i, da lalacewa, da watsuwar laifuffuka, da kuma watsuwar cututtuka. Hakika mu addininmu ya yi gargadi game da shi, gargadi mai yawa, ya hana huduwar mata da maza, a wuraren ibada da masallatai, da wuraren ambaton Allah, duk da cewa a wadannan wuraren mutum ya kan kasance ya shagala da idaba, yana ganawa da Ubangiji, yana rokonsa, yana mai kaskantar da kansa.

Wane nau'i ne na mutane suke zuwa masallatai? Tabbas su ne mutanen kwarai. An karbo Hadisi daga Abu Huraira (R.A) ya ce: "Manzon Allah ya ce: Mafi alherin sahun maza shi ne na farko, kuma mafi sharrin sa shi ne na karshe, kuma mafi alherin sahun mata shi ne na karshe, mafi sharrinsa shi ne na farko.

Sai wadannan sahun guda biyu suka zama mafi sharrin sahu, saboda sun yi kusa da juna, to ina ga haduwar maza da mata a wuraren hutawa, ko wuraren cin abinci, ko wuraren hira? Hatta daga masallaci Manzon Allah ya koya mana maza su jira mata su fara fita, saboda a hana haduwar su a hanya. An karbo daga Hind bintul Harith, lalle Ummu Salama ta bata labari cewa: "Lalle mata a zamanin Manzon Allah (S.A.W) sun kasance idan an yi sallama, sai su mike, sai kuma Manzon Allah (S.A.W) ya jira tare da mazan da suka yi salla tare da shi na wani lokaci, idan Manzon Allah ya mike sai sauran mazan su mike."

Kuma Manzon Allah (S.A.W) ya taba umurtan wani ya bar jihadi don ya tafi hajji tare da matarsa, duk ana wannan ne sadoba kar matar ta cakuda da wasu mazan. An karbo Hadisi daga Ibnu Abbas (R.A) lalle ya ji Manzon Allah (S.A.W) yana cewa: "Kada wani namiji ya kadaita da wata mace ko ta yi tafiya, face a tare da ita akwai muharraminta. Sai wani mutum ya tashi ya ce: Ya Manzon Allah (S.A.W) lalle ni an rubuta ni cikin wadanda zasu tafi jihadi, gashi kuma matata ta tafi hajji ita kadai, sai Manzon Allah (S.A.W) ya ce mishi: tafi kayi hajji tare da matarka."

Kuma Manzon Allah ya hana maza shiga wurin matar da ba muharramarsu ba ce, ko da 'yar'uwarsu ce ita. An karbo Hadisi daga Ukbata bni Amir (R.A) lalle Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Ina jan kunnenku game da shiga wurin mata, sai wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah shin abokin wasa fa (ko wani dan'uwanta ko dan'uwan mijinta?) Sai Manzon Allah (S.A.W) ya ce: Abokin

wasa (ko dan'uwanta ko dan'uwan mijinta wanda ba muharraminta ne ba) ai mutuwa ne!"

Manzon Allah (S.A.W) ya kwatanta shigar dan'uwan miji wurin mace ko dan'uwanta wanda ba muharrami yake a gareta ba, da mutuwa! saboda hadarin da abin yake tattare da shi, da tsananin tasirin da abin yake da shi. Duk da cewa da wuya wani abu ya faru da ita, a zaton mafiya yawan mutane.

Ya yi bayani cewa haduwar mace da wani namiji ba abin natsuwa ba ne, ko da sun kasance dukkansu mutanen kirki, sai ya ce: "Kada wani namiji ya kebanta da wata mace don shaidan sai ya zama na ukunsu".

Ka sani barna tana kara yawa a kasashen da maza da mata suke hade, karuwa mai ban tsoro! Gidajen rainon yara sun fara kuka da yawan 'ya'yan shegu, asibitocinsu suna kuka da yawan cututtukan da jima'i barkatai yake kawowa, kuma tarihi ya tabbatar da cewa babu wata al'umma da maza da matansu za su cakuda face sai sun rasa

cigabansu, kuma a rasa tsaro, kuma barna ta watsu a cikinsu, kuma kamun kai ya tafi abin shi, daga nan sai kaga sun fada cikin barna, kuma annobar zamani (Aids) mai wuyar magani, ta same su.

Wadannan dalilan da wasunsu, su suka sa kasashen duniya suka fara tunanin hanyoyin gyara.

An yi rubuce-rubuce da dama game da matsalolin da ke faruwa sabili da ficewar mata daga gidajensu na aure. Kuma dubban mata ne suka tashi tsaye suna neman mafita game da wannan matsalar. Kuma an yi tarurruka masu dama, a kan abubuwan da fitar mace daga gida da barin aikin da Allah ya dora mata na tarbiyya ya jawo, aikin da babu wanda zai iya yin sa -ko da mai gidan ne da kansa- sai dai ita dole.

Ya dan'uwa, Ya ke 'yar'uwa, ashe ba za muyi alfahari da addininmu ba, kuma mu koma karantarwar Annabinmu (S.A.W). kuma mu rike

Littafin Allah da sunnar Annabinmu (S.A.W) mai tsara mana rayuwa?

Hakika lokaci ya yi da Musulmi za su farka daga baccin da suke yi, su rike hasken shiriya da Allah ya ba su. Har yaushe zamu cigaba da zama a baya, bayan mun kasance masu jagorancin duniya? A haka ne za mu zama shuwagabanni a duniya alhali muna koyon tsarin rayuwa daga bolar turawan yamma? Abin mamaki wai mai mutunci yana koyon rayuwa daga kaskantacce, mai rabo yana kwaikwayon tababbe. Kuma mai girma yana kwaikwayon wulakantacce. Kuma nagari yana kwaikwayon lalatacce. Musulmi yana kwaikwayon kafiri!

Ya wajaba mu fito fili mu gaya wa duniya, da babbar murya, mu gaya musu cewa, mu ne muke da maganin matsalar da duniya ta fada ciki, addininmu shi ne addinin jin kai ga talikai gaba daya, kuma mu zama masu jagorancin duniya zuwa ga alheri da samun rabo da kuma shiriya. Allah yana cewa:

وما أرسلناك إلا رحمة للعلمين (الأنبياء ١٠٧)

Ma'ana: "Kuma bamu aike ka ba face domin wata rahama ga talika"i. (Anbaya'i 107)

Kuma ya ce:

إن هو إلا ذكر للعالمين (ص ٨٧)

Ma'ana: Shi (Alkur'ani) bai zama ba face ambatone ga dukkan halitta". (Sad 87)

Shin bayan wannan bayani za a sami musulmar da ta yi imani da Allah shi ne Ubangiji kuma musulunci shi ne addinin (gaskiya) kuma ta yi imani Annabi Muhammad (S.A.W) Manzon Allah ne, sa'an nan ta rinka kafada da kafada da maza? Shin Musulmi zai yi tunanin mace mai hankali kuma mai kamun kai, kuma wadda ta san abin da take yi, tana jin daukaka da addininta, kuma tana alfahari da musuluncinta, sa'an nan ta yi kafada da kafada da maza?

## SAKO NA GOMA

Shin ka sani Ya kai dan'uwa mai girma –Allah ya kare ka daga kowane sharri da fasadi- dan

sakon sharri, kuma kofar fitina, kuma mai gusar da hankalin jama'a, kuma mai shagaltar da mutane, shi ne kide-kide da wake-wake?

Wannan ciwo da ya dade yana sa su cibaya, kuma ya kwace cigaba, da cin nasara a hannunsu, kuma ya wasa masu sha'awarsu, kuma zukata suka ratayu da shi fiye da ratayuwar da suka yi wa abinci da abin sha. Saboda da shi wasu suke yin soyayya, wasu kuma suke gaba.

Kuma tarihi ya tabbatar da cewa babu wata al'umma da za ta nitsa cikin kide-kide da wake-wake face sai rauni ya same ta, da lalacewar dabi'a, kamar yadda muka sani ga al'ummar Roma da Farisawa. Kuma kamar yadda muke gani ga turawan yamma a yau, miyagun cututtuka sun kama su. Saboda jin kida yana tsokano sha'awar mutum, kuma ya wasa ta. Sai da'a ga Allah ta yi masa wuya, sha'awarsa ta karfafa, kuma dadin duniya ya girmama a cikin ransa, ya manta lahira, da aiki domin ta. Hakika wannan al'umma ta bi, da yawa daga cikin al'adun

wadanda suka gabace ta. Sai ka ga mafi yawan mutane ba su iya rabuwa da kida, a gidajensu, da motocin su, da ofisoshinsu, da kuma kasuwanninsu.

Wannan fa duk da cewa sun san akwai dalilai na shari'a masu yawa da suka zo da haramcin hakan, saboda hakan ya saba wa ruhin musulunci na gaskiya, kuma mai tsarki.

To ga sako zuwa ga masu tsayawa inda Allah ya tsaida su, zuwa ga wadanda suke bayyana cikakkiyar biyayyar su ga Allah da ManzonSa, kuma suke mika jagorancinsu zuwa ga Allah da Manzonsa, kuma suke saba wa sha'awarsu da abin da rayukansu suke so, da kuma al'adunsu da abubuwan da suka gada, idan sun ci karo da shiriyar musulunci, zuwa ga muminai:

إنما المؤمنون الذين إذا ذكر الله وجلت قلوبهم وإذا تليت عليهم آياته زادتهم إيمانا وعلى ربهم يتوكلون (الأنفال ٢)

Ma'ana: "Abin sani kawai, muminai su ne wadanda suke idan an ambaci Allah zukatansu suna firgita, kuma idan an karanta ayoyinSa, a

kansu su kara musu wani imani, kuma ga Ubangijinsu suke dogara." (Anfal 2)

Zuwa ga wadannan gaba daya muke koro hukuncin Allah ga wannan abin kin da ya zama wurin wasu mutane kamar sanannen abu (a shari'a). Allah yana cewa:

ومن الناس من يشتري لهو الحديث ليضل عن سبيل الله بغير علم ويتخذها هزوا أولئك لهم عذاب مهين (لقمان ٦)

Ma'ana: "Kuma akwai daga cikin mutane, wanda ke sayen tatsunniyoyi domin ya batar da mutane daga hanyar Allah, ba da wani ilimi ba, kuma ya rike ta abin izgili! Wadancan suna da wata azaba mai wula kantarwa. (Lukman 6)

Hakika sahabbai sun fassara "lahwal hadith" da waka! Hadisi ya inganta daga Ibnu Mas'ud (R.A) kamar yadda Ibnu Abi Shaiba da Ibnu Jarir da Hakim da wasunsu suka ruwaito, daga Abus Sahba'i, lalle shi ya ji Ibnu Mas'ud (R.A) ana tambayarsa a kan wannan aya, sai ya ce: "Waka ce, na rantse da Allah wanda babu abin bauta

bisa cancanta sai shi." Yana maimaita ha kan sau uku".

Kuma ya inganta daga Ibnu Abbas (R.A) lalle ya ce: "Shi ne waka da sauraron shi."

A wata riwaya ya ce: "Shi ne waka da abin da ya yi kama da shi."

Hakanan mafi yawan Tabi'ai sun fassara "lahwal hadith" da waka a cikin su akwai: Mujahid, da Ikrima, da Alhasan Albasri, da Sa'id bin Jubair da Katada, da Annakha'i, da wasun su.

Ya zo a cikin ingantaccen Hadisin da Al'imamu Ahmad da wanin sa suka ruwaito, daga Abdullhi bin Amr da kuma Abdullahi bin Abbas (R.A) daga Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Lalle Ubangijina Madaukakin sarki ya haramta mini giya da caca da buga ganga, da goge. (da duk abin da ya yi kama da wadannan, kamar kalangu da garaya da jita da dai sauransu)"

Hakanan an samu a cikin sahihu Muslim daga Abu Huraira (R.A), Lalle Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Kararrawa tana cikin sarewar shaidan".

Bukhari ya ruwaito littafinsa, lalle Manzon Allah (S.A.W) ya ce: Hakika a cikin al'ummata za a samu wasu mutane da suke halatta farji da alhariri da giya da kayan kide-kide. Wasu mutane kuma za su sauka kusa da wani dutse, mai kiwonsu yana zagayo su, da yamma ta yi, wani matalauci ya zo don su taimaka masa, sai suka ce masa ya dawo gobe, sai Allah ya hallaka su, da dare, ya kuma ruguzo dutsen a kansu, sa'an nan ya mayar da wasu daga cikin su birai da aladu, haka za su zauna har ranar kiyama."

"Hira" (da ya zo a cikin Hadisin) ma'anarsa, FARJI wato kinaya a kan zina. Ka duba yadda Manzon Allah ya hada waka da abin da haramcinsa ya zama mutawaturi (shahararre) kamar zina da sanya alhariri, da shan giya. Akwai wani Hadisi Hasan (danganensa mai kyau ne) saboda yawan hanyoyinsa, an karbo shi daga

Sahabbai masu yawa, kamar: Abu Huraira, da A'isha, da Imran bin Husain, da Abu Malik, da Abu Sa'id Alkhudri, da Aliyu bin Abi Dalib, da (Hadisi) Mursal daga Abdurrahman bnu sabid.

Amma Hadisin Abu Huraira, Sa'id bin Mansur da Ibnu Abid Dunya da wasunsu, suka fitar da shi, ya ce Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "A karshen zamani za a maida wasu mutane daga cikin wannan al'umma birai da aladu, sai suka ce: Ya Manzon Allah, shin basu shaida babu abin bauta bisa cancanta sai Allah ba ne, kuma Muhammad (S.A.W) ManzonSa ne? sai ya ce: kwarai sun shaida, kuma suna salla suna azumi kuma suna hajji, sai suka ce: To menene ya same su haka? Sai ya ce: Sun riki kayan kide-kide da dundufa, da mawaka, sai suka kwanta cikin mayensu da wasansu, sai suka wayi gari Allah ya maida su birai da aladu."

Ibnu Abid Dunya da waninsa sun ruwaito daga Ibnu Mas'ud (R.A) ya ce: "Waka tana tsirar

da munafunci a zuciya kamar yadda ruwan sama ke tsirar da shuka".

Sa'id bnu Mansur ya fitar da Hadisi daga hanyar shi Baihaki ma ya fitar, daga Ibnu Abbas (R.A) ya ce: "Dundufa haramun ce, kayan dusa haramun ne, ganga (da kalangu) haramun ne, haka nan sarewa haramun ce."

Dukkan A'imma (shuwagabannin Mazhabobi) sun ittifaki a kan haramcin wake-wake da kide-kide, an tambayi Imam Malik, me ya sa mutanen Madina basu dauki waka a bakin kome ba (wato kamar ba haramun ba)? Sai ya ce: "ai fasikai ne ke yin hakan!"

Amma Mazhabar Imam Abu Hanifa, ta fi kowace mazhaba tsanani game da haramta waka, hakika dalibansa sun bayyana haramcin duk wani kayan wasa, kamar sarewa, da dundufa, da kada molo, (kamar garaya, kukuma da sauransu) kuma suka bayyana cewa wannan sabo ne da ke wajabta fasikanci, kuma ya sa a maida shedar mutum.

Amma Imamush Shafi'i ya ce: "Hakika na bar Bagadaza, munafukai sun tsiro da wani abu suna kiran sa "attagbir" suna hana mutane karatun Alkur'ani saboda shi.

Ibnul Kayyim ya ce: "Idan wannan ne maganar Shafi'i a kan "attagbir" da dalilinsa, cewa yana hana mutane karatun Alkur'ani, duk da cewa shi waka ce, da take sa mutane zuhudu game da rayuwar duniya. wani mai rerawa zai rera, wadanda suke wurin suna dan kada molo a kan shimfidu, da matasai…"

Ibnu Salah ya ce: "Ya kamata a sani lalle dundufa, da busa, da waka, idan suka hadu to sauraran wannan ya haramta, an samo haka daga limaman mazhabobi da wasunsu daga Malaman Musulmi".

Shi kuma Imam Ahmad cewa ya yi: "Waka tana tsirar da munafunci a cikin zuciya. Kuma ya yi bayani cewa a karya duk wani kayan kida, kamar ganga, da sauran su, kuma ya yi bayanin haramcin duk wani amfani da za a samu ta

hanyar waka, da duk wata dukiya da za a karba a kan hakan.

Kuma ka sani Ya kai dan'uwa mai girma – Allah ya kare ka daga duk wani sharri da zunubi-cewa waka, mata kawai aka halatta wa, suma da wadannan sharudda masu zuwa:

1. Maganar kar ta zama akwai alfasha da batsa a cikin ta.

2. A buga dundufa kawai banda sauran kayan kide-kiden domin sun haramta.

3. Ya kasance ranar idi ne ko ranar bukin aure.

4. Kuma wurin ya kasance mata ne zalla babu maza.

Dalili a kan haka shi ne abin da Nasa'i da Dayalisi da Ibnu Abi Shaiba da Hakim da wasunsu suka ruwaito daga Amir bin Sa'ad ya ce: "Na shiga wurin Ibnu Mas'ud da Karzhata bni Ka'ab da Thabit bni Zaid, a tare da su akwai wasu kuyangi suna buga dundufa suna musu waka, sai na ce: "kun yarda da haka, alhali ku sahabban

Manzon Allah (S.A.W) ne? sai ya ce: lalle mu an mana sauki a kan hakan a wurin bukin aure".

A cikin Bukhari da Muslim da wasunsu, daga A'isha (R.A): lalle Abubakar (R.A) ya shiga wurinta ranar babbar salla, ko karama, a lokacin tare da ita akwai Manzon Allah (S.A.W), ga wasu 'yan mata (kanana) biyu daga cikin 'yan matan mutanen Madina, suna waka da abin da mutanen Madina suka fadi ranar yakin "bu'ath" ta ce: amma aslinsu ba mawaka ba ne, sai Abubakar ya ce: Sarewar shaidan a gidan Manzon Allah (S.A.W)? Sai Manzon Allah (S.A.W) ya ce: Ya Abubakar, lalle kowadanne mutane suna da idinsu mu ma wannan ne idinmu.

Kuma wadannan 'yan mata kanana suna waka ne ranar salla, da wata waka da aka fadi lokacin yaki.

Ya dan'uwana abin kaunata, dan tsaya kadan tare da ni, kusa da wadannan ayoyi biyu, kana mai tunani da kawo hankalinka kusa. Allah ya ce:

إنمـا يسـتجيب الـذين يسـمعون والمـوتى يبعـثهم الله ثـم إليـه ترجعـون (الأنعام ٣٦)

Ma'ana: "Abin sani kawai, wadanda suke saurare ne suke karbawa, kuma matattu Allah yake tayar da su, san' nan zuwa gare shi ake mayar da su". (An'am 36)

Kuma ya sake cewa:

فإن لم يستجيبوا لك فاعلم أنما يتبعون أهواءهم ومـن أضـل ممـن اتبـع هواه بغير هدى من الله إن الله لا يهدي القوم الظالمين (القصص ٥٠)

Ma'ana: "To idan ba su karba maka ba, to ka sani suna bin son zuciyarsu ne kawai, kuma wanene mafi bata daga wanda ya bi son zuciyarsa, ba tare da wata shiriya daga Allah ba? Lalle ne, Allah ba ya shiryar da mutane Azzalumai". (Kasas 50)

A ingantaccen Hadisi da Imam Ahmad ya ruwaito a musnad, da Abu Dawud a sunan da wanin su, daga Ibnu Umar (R.A) daga Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Duk wanda ya yi gardama a kan barna (ko karya) ba zai gushe a cikin fushin Allah ba, har sai ya bari".

A karshe ka sani Ya kai dan'uwa Alhaji –Allah ya kiyaye ka, kuma ya datar da kai- lalle Manzon Allah (S.A.W) ya ce: "Duk wanda ya yi hajji, bai yi batsa (ko jima'i) ba, kuma bai yi wani fasikanci ba, to zai koma tamkar ranar da mahafiyasa ta haife shi."

Kuma ya sake cewa: "Duk wanda ya yi hajji mabrur (kubutacce) ba shi da sakamako sai aljanna."

Idan Allah ya sa ka sami wannan lada mai girma, to wallahi ka zama mai girma abin daukakawa, to ina jan kunneka kar ka fara ka rusa shi, da saba wa Allah, da barin yi masa biyayya, domin yana daga cikin alamun an karbi hajjinka, ka bi shi da kyawawan ayyuka, kuma yana daga cikin alamun mayar ma da hajji, ka rinka yin sabo bayansa, da yin sakaci da ayyuka na gari, kada rabonka a aikin hajji ya zama lakabi kawai, don ace: "Alhaji wane" don wallahi wannan ba zai amfane ka a wurin Allah ba, kamar yau ne za ka bar duniya! Anan ne za ka san cewa

amfanin aiki a wurinka shi ne a karba, ba shakali ko lakabi ba.

Allah ya sanya hajjinka karbabbe ne, kuma ya gafarta maka zunubbanka, kuma ya karbi ayyukanka, kuma ya mayar da kai zuwa wurin iyalinka, da 'ya'yanka, da garinka lafiya, kana mai cin nasara. Allah shi kadai ya isa ya yi hakan.

Allah ya yi dadin tsira da aminci bisa AnnabinSa Muhammad tare da mutanen gidansa baki daya, kuma dukkan godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, kuma karshe mai kyau yana ga masu tsoron Allah ne.